Me Ake Nufi Da A Sake Haifar Mutum?

Muhimman Tambayoyi

R.C. SPROUL

Me Ake Nufi Da A Sake Haifar Mutum?

Me Ake Nufi Da A Sake Haifar Mutum?

R.C. SPROUL

Me Ake Nufi Da A Sake Haifar Mutum?

Asali an buga shi da Turanci a ƙarƙashin taken:

What Does It Mean to Be Born Again?

© 2010 na R.C. Sproul

Ma'aikatar Ministirin Ligonier ce ta buga shi

421 Ligonier Court, Sanford, FL 32771, U.S.A.

www.ligonier.org

An yi amfani da shi tare da izini. An kayyade duka ikon hakkin mallaka.

Lux In Tenebris ne ya fassara kuma ya buga a Najeriya

LIT Publication

19 Ikorodu Rd Maryland, Lagos Nigeria

+234-803-262-7069

Abubuwan da ke Ciki

Daya: Dole Ne In Sami Sabon Haihuwa?.....1

Biyu: Sabon Haifuwa Asiri Ne.....13

Uku: Sabon Haihuwa Ita Ce Mafari.....26

Hudu: Sabon Haihuwa Aikin Allah Ne Mai Cikaken iko 37

Biyar: Sabon Haihuwa Tana Faruwa Nan Take.....46

Shida: Sabon Haihuwa Na Dindindin Ne.....58

Dole Ne In Sami Sabon Haihuwa?

Na taɓa yin magana da wani mutum wanda ya ce yana so ya kara sanin bangaskiyar Kirista. Ya ce shi yana tsammanin shi Kirista ne kuma yana son sanin ƙari game da abin da Kiristanci ya ƙunsa. Amma, ya yi gargaɗi, "Ba na son zama *Kirista mai sabon haihuwa*."

Sa'ad da na ji haka, tunanina ya koma ga yakin neman shugaba kas ana 1976, lokacin da Jimmy Carter ya bayyana kansa a matsayin Krista mai sabon haihuwa. Kusan a wannan lokaci guda, Charles Colson, wanda ya kasance mai ba wa Shugaba Nixon shawara kuma wanda ya shiga cikin rikicin Watergate, ya koma ga Kristi kuma ya *rubuta littafi* mai suna Born Again, wanda aka sayar da kwafinsa miliyan da yawa kuma aka mayar da shi fim da suna guda. Shugaban Black Panther Eldridge Cleaver har ma da Larry Flynt, mawallafin *mujallar Hustler,* su ma sun shiga ta hanyar sanar wa duniya

cewa su ma an “sake haife su,” ko da yake Flynt yanzu yana kiran kansa mara addini.

Nan da nan sai kalmar nan '*sabon haihuwa*', wadda aka sani kawai a tsakanin wani ƙaramin sashe na ikklisiya, ta zama babban labari mai dumi kuma ta fara samun hankalin ƙasa baki ɗaya. An aro wannan kalma daga duniya marasa addini inda aka yi amfani da ita ga abubuwan da ba na bangaskiyar Kirista ba. Misali, idan ɗan wasan ƙwallon baseball ya yi shekara mai kyau bayan ya fuskanci wata shekara marar kyau, sai a ce shi ɗan wasa ne “da aka Haifa sabo.”

Duk da haka, a wani wurin cikin wannan hayaniyar, sai ainihin ma’anar *kalmar nan sake* haihuwa ta zama a lulluɓe. Sakamakon haka, akwai rudani mai yawa, har ma a cikin ikklisiya, game da hakikanin yanayin sabuwar haihuwa. Manufar wannan ɗan littafin, ita ce a bincika abin da ake nufi, ta fuskar Littafi Mai Tsarki da kuma tauhidi, mutum ya kasance kasance-wa an sake haife shi.

A farko, dole ne in lura cewa furucin nan “Kiristan da aka sake haifa,” idan aka dauke ta a ma’ana ta musamman kuma ta ilimi, Magana ce da ta maimaita abu daya. Wannan haka yake domin, bisa ga Sabon Alkawari, domin mutum ya zama Kiris-ta, dole ne sai an sake haifarsa (Yohanna 3:3–5). Saboda haka, idan an sake haifi mutum, shi ko ita Kirista ne. Don haka, kiran mutum “Kiristan da aka sake haifa” kamar kana cewa wannan mutum

“Kirista Kirista ne.” Sabon Alkawari bai san wani nau’in Kirista ba in ban da wannan.

Haka kuma, kalmar nan *sake haifuwa* sanannen lafazi ne mai ma’ana ɗaya da kalmar *tauhidi wato sabon haihuwa ta ruhaniya*. Ban san da wata ikklisiya ba a tarihin Kiristanci da ba ta da koyarwar sabon haihuwa ko kuma sake-haihuwa. Wato, kowace ƙungiyar Kirista a tarihin Yamma ta gina wani nau’in fahimta game da abin da ake nufi da sake haifuwa a fannin ruhu. Wannan haka yake domin manufar ba ta samo asali daga masana tauhidi, masu sharhin Littafi Mai Tsarki, ko masu wa’azi ba. Tushen ra’ayin nan na sake haihuwa ta fannin ruhu yana cikin koyarwar Yesu. Tun da yake Kiristoci suna bayyana kansu a matsayin masu bin Almasihu, a dabi’ance sun nuna sha’awar fahimtar abin da Yesu yake faɗa game da wannan ra’ayi.

Tattaunawar Yesu da Nikodimus

Labarin koyarwar farko ta Yesu a kan wannan batu yana cikin Yahaya 3. Ina so mu bi wannan nassi dalla-dalla domin mu sami tushe mai ƙarfi don tattaunawarmu ta gaba game da sake haifuwa.

Yahaya ya rubuta cewa, “Akwai wani Bafarisiye mai suna Nikodimus, wani ɗan majalisar Yahudawa. Ya zo wurin Yesu da dad dare” (1–2a).

Nan da nan Yahaya ya gabatar mana da Nikodimus kuma ya gaya mana abubuwa biyu game da tarihinsa: na farko, shi Bafarisi ne, na biyu kuma, shi shugaban Yahudawa ne. Farisawa rukunin addini ne masu ra'ayin mazan jiya waɗanda aka san su da kiyaye dokar Allah sosai. “Shugabannin Yahudawa” su ne hukumomin addini a Isra'ila. Al'ummar Yahudawa tana ƙarƙashin ikon masarautar Roma kuma gwamnan Roma ne yake mulka su. Sai dai, an ba wa wata ƙungiya ta mutane saba'in ikon addini a Isra'ila waɗanda suka kafa wata hukuma da aka sani da Sanhedrin. Waɗannan mutanen sun yi daidai da sanatoci a Amurka ko kuma manyan malaman darikar Katolika (cardinals). Sa’ad da Yahaya ya bayyana Nikodimus a matsayin shugaban Yahudawa, a sarari yake nuna cewa Nikodimus ɗan majalisar Sanhedrin ne. Ba duka Farisawa ne mambobin Sanhedrin ba, amma wasu mambobin Sanhedrin Farisawa ne. Don haka Nikodimus mutum ne mai ilimi da iko, wanda aka horar da shi sosai a fannin ilimin tauhidi.

Nikodimus ya zo wurin Yesu da dare. Me ya sa ya yi hakan? Ina da tunanin cewa Nikodimus yana ɗan fargaba ne. Ba ya son a gan shi tare da Yesu a gaban jama’a, wanda ya shahara a wurin mutane amma hukumomin addini suna zarginsa. Don haka ya yi taka-tsan-tsan a gamuwarsa ta farko da Yesu.

Duk da haka, ya zo da kalamai masu daɗi: “Rabbi, mun sani kai malami ne daga Allah. Gama ba wanda zai iya yin waɗannan abubuwan banmamaki da kake yi in Allah ba ya tare da shi.” (v.2).

Abu ne mai muhimmanci cewa wannan shugaban Yahudawa ya amince da Yesu a matsayin rabi kuma ya yi masa magana cikin daraja wadda aka tanada domin masanin ilimin tauhidi. Nikodimus ya amince cewa Yesu ingantaccen malami ne na Maganar Allah. Bayan haka ya ci gaba da bayyana cewa aƙalla wasu daga cikin shugabannin Yahudawa sun gane cewa Yesu malami ne da Allah ya aiko, albarkacin alamun da yake yi. Wannan hali ya bambanta ƙwarai da na mutane da yawa a cikin ƙungiyar Farisawa. Ba su da irin wannan kyakkyawan ra'ayi game da Yesu. Hasali ma, sun jingina ayyukansa na ban mamaki ga ikon Shaiɗan (Mat. 12:22-32). Amma wannan Bafarisun ya ƙi yin irin wannan kazafi mai muni; maimakon haka, ya zo ne yana yabon Yesu. Yana cewa ne, “Yesu, na gane cewa lalle kai malami ne da aka aiko daga wurin Allah domin babu mutumin da zai iya nuna irin ikon da ka nuna sai dai idan Allah yana tabbatar da saƙonsa.”

Sharaɗi Mai Mahimmanci

Ka lura da yadda Yesu ya amsa. Bai ce, “Na kaskantar da kaina saboda wannan daraja da ka ba ni ba, ya kai shugaban Yahudawa, ɗan majalisar Sanhedrin; abin farin ciki ne mutum mai babban matsayi kamar ka ya yabe ni.” Kusan kamar Yesu ba zai iya jira Nikodimus ya gama yi masa yabo ba ne. Da zarar Nikodimus ya yi shiru, Yesu ya amsa kamar yadda ya saba yi a koyarwarsa—ta hanyar watsar da maganganu marasa mahimmanci da shiga kai tsaye cikin zuciyar al’amarin.

Ya ce wa Nikodimus, “Gaskiya nake faɗa maka, ba wanda zai iya ganin mulkin Allah sai an sāke haihuwarsa.” (v.3). Ma'ana: “Nikodimus, daina magana game da al'amuran da ba su da muhimmanci da darajoji na mutum. Abin da nake so in sanar da kai shi ne: Akwai wani abu da dole ne mutum ya yi domin ya ga mulkin Allah.”

A cikin ilimin tauhidi da falsafa, muna jin daɗin bambance abubuwa, kuma bambanci ɗaya mai matuƙar mahimmanci a cikin waɗannan fannoni shi ne tsakanin abin da muke kira “sharaɗi mai mahimmanci” da kuma “sharaɗi wadatacce.” An bayyana sharaɗi mai mahimmanci a matsayin abin da dole ne ya faru kafin wani abu dabam ya biyo baya. Misali, domin wuta ta kone, kasancewar iskar oxygen sharaɗi ne da yake wajibi. Idan babu oxygen, ba za a iya samun wuta ba. Akasin haka, sharaɗi wadatacce shi ne duk abin da ake buƙata domin sakamako ya faru. Iskar oxygen ba sharaɗi ne wadatacce ga wuta ba. Tana da mahimmanci ga wuta, amma ita kaɗai ba ta tabbatar da samun sakamakon wuta ba. Ba za ka iya samun wuta ba tare da oxygen ba, amma za ka iya samun oxygen ba tare da samun wuta ba. A takaice, sharaɗi mai mahimmanci shi ne *sine qua non*—wato abin da in babu shi, sakamakon da ake buƙata ba zai biyo baya ba.

Yesu ya bayar da sharaɗi mai mahimmanci a cikin wannan tattaunawa da Nikodimus. Duk lokacin da Yesu ya koyar da sharaɗi mai mahimmanci, ya kamata mu kasa kunne sosai,

amma hakan ya fi zama gaskiya a wannan yanayi domin Shi ya bayyana wani sharaɗi na dole domin shiga cikin mulkin Allah. Ya ce, “In ba a sake haifar mutum ba, ba zai iya ganin mulkin Allah ba.” Wato, in har “A” ba ta faru ba, “B” ba za ta taba biyo baya ba. Ko kun fahimci dalilin da ya sa hakan yake da ma-himmanci? Da waɗannan kalmomi, Yesu ya shimfiɗa sharaɗi mai mahimmanci na shiga cikin mulkinsa. Ya katse wannan mutumin da aka horar da shi sosai a fannin tauhidi, wanda yake shugaban addini ne, wanda kuma yan ƙasarsa a Isra’ila suke girmama shi kuma suke yaba masa, sannan ya doke shi da gaskiya kai tsaye: “Kana bukatar a sake haifarka.” Kamar dai ni ne zan shiga cikin ikklisiya wani fasto ne, kuma yayin da yake yi mini tambaya game da tauhidi ko kuma yake faɗa mini wata magana ta kirki, sai in ce masa: “Dakata tukunna.” Ba za ka iya ma ganin mulkin Allah ba domin kana bukatar a sake haifarka.” Ba abin mamaki ba ne da Farisawa suka nuna ƙiyayya sosai ga Yesu.

In bayyana shi a mafi sauƙin ganewa, idan ba a sake hai-farka ta ruhaniya ba, ba ka zama Kirista ba. Wajibi ne a sake haifarka domin ka zama Kirista. Babu wanda aka haifa a mat-sayin Kirista. Babu wanda yake shigowa wannan duniya tuni yana cikin mulkin Allah. Farisawa sun zata cewa an haife su ne a cikin mulkin Allah. Suna tunanin: “Mu ’ya’yan Ibrahim ne. Muna yin dukan abubuwan da suka dace. Muna da dokar Musa.” Amma daga baya Yesu zai ce musu: “Ba ku ba ne ’ya’yan Ibrahim. Ku ’ya’yan uban da kuke bauta wa ne” (duba Yohanna 8:39-47).

Ba zan iya nanata yadda wannan furuci na Yesu yake da tsauri sosai ba. Yana da sauti yana da tsauri a kunnuwanmu, kuma ya ma fi zama da tsauri ga mutanen zamanin Kristi.

Ka tuna da abokina wanda ya ce, “R.C., ina son in zama Kirista, amma ba na son in zama Kirista wanda aka sake haihuwa.” A zahiri, yana son ya samu abubuwa biyu ne lokaci guda koda kuwa sun saba wa juna. Akwai yiwuwar cewa abin da yake nufi kawai shi ne, “Ina son in zama Kirista, Kirista na gaske, amma ba na son in zama ɗaya daga cikin waɗancan mutanen da suke fito da addininsu fili har su addabi wasu da hanyoyinsu na bishara masu ban haushi.” Wannan shi ne yadda ya ke rarrabe rukunin Kiristoci da suka sa shi jin takura, salon rayuwa a cikin ikklisiya Kirista wanda yake gani a matsayin sifa ta musamman ga “Kiristoci waɗanda aka sake haihuwa.”

Amma a ainihin ma’anar harshen, akwai nau’in Kirista guda ɗaya kawai. Akwai salo daban-daban na wannan nau’in Kirista guda ɗayan. Wasu suna da ladabi wasu kuma marasa kunya ne. Wasu masu shiru ne wasu kuma masu yawan hayaniya ne.

Wasu masu ra’ayin mazan jiya ne wasu kuma ba masu ra’ayin mazan jiya sosai ba ne. Amma nau’i guda ɗaya tilas da ke shiga mulkin Allah shi ne wanda aka sake haifa, domin Yesu ya maida sake haifuwa ya zama dole. Saboda haka, abu na farko da nake son bayyanawa game da sake haihuwa shi ne cewa abu ne na dole.

Yadda Yesu Ya Yi Amfani da Maimaitawa

Yahudawa suna da hanyoyi guda biyu da suke amfani da maimaitawa domin jaddadawa, kuma Yesu ya yi amfani da su duka biyun a cikin tattaunawarsa da Nikodimus. Na bincika ɗaya daga cikin *waɗannan* hanyoyin a cikin littafina mai suna *Tsarkin Allah* sa'ad da na yi nazarin littafin Isaya babi na 6, inda aka kwatanta seraphim a cikin ɗakin kursiyin Allah na Sama suna rera taken "Mai tsarki, mai tsarki, mai tsarki" a matsayin martani na bi-da-bi. Na bayyana mahimmancin wannan maimaita kalma, dabarar da muke gani ana amfani da ita a ko'ina cikin Littafi Mai Tsarki. Sa'ad da Yahudawa suke son su jaddada wani abu, maimakon su ƙara alamar mamaki ko kuma su yi amfani da rubutu mai karkata, sai su maimaita shi kawai.

Sa'ad da Yesu ya gabatar da wannan sharaɗi na dole, bai ce kawai, "In ba an sake haifar mutum ba, ba zai iya ganin mulkin Allah ba." Maimakon haka, ya fara ne da cewa, "Gaskiya, gaskiya," *wanda* a yaren asali, za a *karanta* shi ne a matsayin, "amin," "amin." Mun sami kalmar nan amin daga wannan kalmar Ibrananci; kalma ce da muke yawan amfani da ita wajen kammala addu'o'inmu, wadda da ita muke nufin, "Gaskiya" ko "Bari ya kasance haka." Lokaci zuwa lokaci, Yesu yakan *gabatar* da koyarwarsa ta hanyar maimaita kalmar nan amin, kuma wannan yana ɗaya daga cikin waɗancan lokuta. Sa'ad da Yesu ya ce, "Gaskiya, gaskiya," kamar yana cewa ne, "Zai fi kyau ka saka alamar tauraro a kusa da

wannan domin yana da muhimmanci ƙwarai da gaske.”

A cikin azuzuwan da nake koyarwa a makarantar tauhidi, na kasance ina gaya wa ɗalibaina, “Duk lokacin da kuka ga na rubuta wani abu a jikin allo, ya kamata ku saka alamar ‘X’ ja a kusa da shi a cikin bayanan da kuke ɗauka, domin kuna iya tabbata cewa zai fito a jarrabawa.” Yesu ya yi wani abu mai kama da haka sa’ad da ya ce, “Gaskiya, gaskiya.” Sa’ad da yake son ya ce, “Ga wani abu da yake da muhimmanci kwarai,” sai ya ce, “Gaskiya, gaskiya.”

Akwai dubban ma’aikatan bishara a Amurka waɗanda za su tashi tsaye a wannan safiyar Lahadi su ce ba lallai ba ne a sake haifar mutum domin ya shiga mulkin Allah. Idan kun ji wani ya faɗi haka, bari in tambaye ku da ku tuna cewa ba abin da Yesu ya faɗa ba ne ke nan. Sa’ad da kuka ji rikicewa game da ko sake haihuwa wajibi ne ko a’a, za ku zama dole ku yanke shawarar wanda yake magana da mafi daukakar iko ga ikklisiya Kirista. Ubangijin ikklisiya ya ce, tare da jaddadawa, “Gaskiya, gaskiya, ina gaya muku, idan ba an sake haifar mutum ba, ba zai iya ganin mulkin Allah ba.”

Akwai hanya ta biyu da Yahudawa suke amfani da maimaitawa. Baya ga maimaita kalma, sukan maimaita wani ra’ayi na musamman da lafazi ɗan daban. Sa’ad da manzo Bulus yake yi wa Galatiyawa gargaɗi game da watsar da bisharar nassi, ya ce musu, “Amma ko mu, ko mala’ika daga sama ya yi wa’azin wata bishara dabam da wadda muka yi muku, bari yă zama la’ananne har abada!” (Gal. 1:8).

Sa'an nan manzon ya ƙara da cewa, "haka yanzu ma ina ƙara cewa in wani yana muku wa'azin wata bishara dabam da wadda kuka karɓa, bari yă zama la'ananne har abada!" (st. 9). Bulus ya yi amfani da nau'i na biyu na maimaitawar Yahudawa a nan, yana bayyana ra'ayi ɗaya sau biyu da kalmomi ɗan daban.

Yesu ya yi hakan ma. Da farko ya ce, "Gaskiya nake faɗa maka, ba wanda zai iya ganin mulkin Allah sai an sāke haihuwarsa." (Yohanna 3:3). Nikodimus ya amsa ya ce: "Yaya za a haifi mutum sa'ad da ya tsufa? Tabbatacce ba zai sāke koma sau na biyu a cikin mahaifiyarsa don a haife shi kuma ba!" (st. 4). Sa'an nan Yesu ya amsa, "Gaskiya nake faɗa maka, ba wanda zai iya ganin mulkin Allah sai an haife shi ta wurin ruwa da kuma Ruhu." (st. 5). Maimaita wannan babban sharadi da Ubangiji ya yi ya nuna muhimmancinsa ƙwarai.

Ga abin da na fahimta daga koyarwar Yesu Kristi: Ba zai yiwu a ga mulki ko a shiga mulkin ba sai dai idan an sake haifar mutum. Amma hakan ya tada wata muhimmiyar tambaya: Mene ne ma'anar "sake haifuwa"? Kamar yadda na faɗa a baya, kowace ikklisiya tana da wata koyarwa game da sabon haihuwa a ruhaniya. Ku yarda da ni, ba duka ba ne suke da koyarwa iri ɗaya. Dukkansu sun amince cewa sabon haihuwa na ruhaniya ko sake haifuwa sharadi ne na shiga mulkin Allah, amma ba duka ba ne suka amince a kan yadda ake cika wannan sharadi da kuma ainihin abin da hakan ya ƙunsa ba. A surorin da za su biyo baya, za mu karkata

hankalinmu wajen tantance ainihin abin da Yesu yake nufi sa’ad da ya kafa wannan sharadi mai mahimmanci.

Sabon Haifuwa Asiri Ne

Na taɓa ganin wani mai zane a talabijin yana yin zane nuna yadda ake yi. Yayin da yake zanen, ya bayyana dabarun da yake amfani da su. Ya fara ne da zanen wasu manyan gizagizai masu kumbura. Bayan haka, ya nuna yadda ake amfani da wani nau'in burtushin daban don yi wa gizagizai inuwa da kuma ƙara musu kwarkwarori. Ya nuna cewa akwai bambanci tsakanin hoton gizagizai da ke tsaye cak a sararin sama da kuma gizagizai da iska ke kora. Waɗanda ke tsaye cak suna kama da waɗanda suka shanye—sun daskare a jikin zanen, kamar yadda yake. Mutumin ya bayyana cewa, ainihin gizagizai ba wai kawai suna ɗauke da danshi ba ne, har ma iska tana kora su. Daga nan sai ya ɗauki burtushi na uku, ya motsa hannunsa ta yadda zai ƙara wasu alamomi (kusan layuka) a saman gizagizai. Layukan ba su kasance daidai da juna ba, amma sun fayyace gefen gizagizai sarai. Lokacin da ya kammala, gizagizai suka bayyana kamar suna motsi suna kuma juyawa sama.

Na kusan ji n motsin iskar a cikin hoton, ko da yake ba na iya ganin iskar kanta ba.

Bayan ya koyar da Nikodimus game da matukar bukatar na sake haifuwa, Yesu ya ci gaba da yin kwatanci tsakanin iska da kuma asirtaccen aikin zuciya na ban al'ajabi na sake haifuwa ta ruhaniya. A cikin wannan babi, za mu mayar da hankali ne a kan wannan fanni na Sake haifuwa.

"Ruhu Mai Tsarki ne Ya aikata duka"

Shekaru da dama da suka gabata, na sami damar yin magana na tsawon sa'a guda a kebe da wani mutum wanda a baya na taba haduwa da shi na dan lokaci kalilan sau daya kacal. Mutumin shi ne mai wa'azin bishara Billy Graham. Na sami damar cin abincin dare tare da shi a Asheville, North Carolina. Mun tattauna abubuwa da dama a wannan lokacin, amma a tsakiyar tattaunawarmu, bayan kowannenmu ya bayyana labarin juyowarmu ga Allah, Billy ya ba ni labarin abin da ya faru da shi sa'ad da yake saurayi sa'ad da ya kasance ƙarƙashin tasirin wa'azin Mordecai Ham, wani mai jawabi da yake gudanar da jerin tarukan wa'azi a Charlotte, North Carolina. Billy ya ambaci wannan lokaci na rayuwarsa sau da dama a cikin huɗubobi da littattafai, amma jin sa daga gare shi da kansa bayan duk waɗannan shekaru ya kasance abin ƙanƙan da kai a gare ni. Abin da ya fito fili a labarinsa shi ne cewa ya bayyana cikin murna game da shi kamar dai abin ya faru a ranar nan ne.

Har yanzu yana cike da sha'awar da aka rura tun shekaru da dama da suka gabata a wannan lokacin da ya hadu da Kristi. Ya bayyana duk abubuwan da ya fuskanta yayin da aka ja hankalinsa zuwa ayyukan ibada na Mista Ham inda ya saurara dare bayan dare har sai da a karshe aka ja shi zuwa ga Kristi ta hanyar da ba zai iya bijirewa ba. A karshe, Billy ya kalle ni ya ce, "Ruhu Mai Tsarki ne ya yi duka." Yana magana ne game da kasancewa sake haifuwa ta wurin Ruhu.

Matata ma tana faɗar abu makamancin haka game da tūbarta. Ni da Vesta mun yi soyayya na kusan shekaru biyar, kuma muna shirin yin aure. Ba zato ba tsammani, a shekarara ta farko a jami'a, na tūba, kuma an gaya mini tun da wuri a cikin tafiyata ta bangaskiya cewa a matsayina na Kirista ba a yarda in auri macen da ba ba ta da bangaskiya ba. Amma Vesta ita ce macen da nake son aura kuma wadda muka riga muka yi alkawarin aure. Wannan ya zama babban rikici a gare ni a wannan lokaci na rayuwata.

A nata ɓangaren, Vesta tana fama da wannan baƙon hali da ya mamaye angonta. A dā ba ni da wani ƙwaƙƙwaran ra'ayi na addini, amma yanzu Kiristanci ya juyar da rayuwata ƙasa-sama. Ba ta sani ba ko hauka nake yi.

'Yan watanni bayan tūbata, Vesta ta yi shirin zuwa ziyarata. A ranar da za ta iso, na fasa zuwa darasi, na zauna a ɗakina, na kuma kulle ƙofar. Na durƙusa a ƙasa kusa da gadona na yi addu'a kamar yadda ban taɓa yin addu'a ba a dā. Na ce,

“Ya Allah, ban san ko mene ne tabbatattun ƙaddarorinka ba, amma idan akwai wani abu a ciki da bai dace da abin da nake so a nan ba, don Allah ka canja shi.” Na yi kokawa da Allah na tsawon sa’o’i a wannan lokacin. A ƙarshe, na yi alkawarin cewa idan Vesta ba ta zama Kirista ba a wannan karshen mako, zan rabu da ita. Na jingina komai a kan wannan.

Sa’ad da Vesta ta iso, muka tafi taron ƙungiyar Kiristoci da nake cikinta. Ban gaya wa Vesta abin da na yi addu’a a kai da kuma abin da na yanke shawara ba. Ban ce, “Duba, idan ba ki zo ga Almasihu ba a wannan ƙarshen mako, ina son zoben ya dawo” ba. Ban ce uffan ba game da hakan. Don haka ta zo taronmu, kuma ba tare da wani rinjaya daga gare ni ba, ta sadu da Almasihu a wannan taron. Lokacin da ta fito daga taron, tana cike da murna ƙwarai. Ta kasance kamar Archimedes lokacin da ya fito daga bahon wanka yana ihu, “Eureka, na same shi!” Ta san abin da kowane Kirista ya sani—farin cikin fansar da aka yi mata.

Amma sa’ad da ta tafi barci, dukan dare ta riƙa farkawa tana mintsini kanta, tana cewa: “Har yanzu yana nan? Har yanzu ina da shi?” Bayan haka sai ta bincika yadda take ji a ciki ta ce, “I, har yanzu yana nan.” Sai ta juya ta koma barci.

Washegari da safe sa’ad da muka haɗu, ta gaya mini abin da ya faru da ita a daren. Sai ta yi mini wannan kalami, wanda ba zan taɓa mantawa da shi ba:

“Yanzu na san ko wane ne Ruhu Mai Tsarki.” Na yi ƙoƙarin bayyana mata abin da ya faru da ni, amma hakan ya kasance kamar ƙoƙarin bayyana bakan gizo ne ga makaho. Sai lokacin da Vesta ta ba da gaskiya kuma ta dogara ga Almasihu ne ta sami fahimta ta kashin kai game da asali da kuma halin Allah Ruhu Mai Tsarki. Ta riga ta ji labarin Ruhun tun da. Ta yi girma tana zuwa ikklisiya akai-akai. Ta sha jin addu’ar albarka da ake yi da sunan Uba, da Ɗa, da kuma Ruhu. Amma dukan waɗannan abubuwa sun kasance biki ne kawai a gare ta; babu wani ainihin gaskiya da ya shafi kanta ko kuma aikace-aikace a tarihinta na addini. Amma sa’ad da aka canza zuciyarta, sai ta san Ruhun.

Wahalar da na fuskanta wajen bayyana juya zuwa ga Allah da na yi ga Vesta ba baƙon abu ba ne. Ɗaya daga cikin abubuwa mafi wahala a duniya a bayyana filla-filla shi ne abin da ake nufi da samun wani abin da ya faru a ruhaniya wanda ya canja rayuwar mutum. Wannan haka yake domin sabonhaihuwa asiri ne. Kuma idan asiri ne ga waɗanda daga cikinmu da suka dandana shi, to ga wadanda ba su taba dandana shi ba – har ma da kwararrun malaman tauhidi kamar Nikodimus – asiri ne mai zurfi sosai wanda ba za a iya fahimta ba a matakin asali.

Sake Haifuwa (ta ruhu) Asiri Ne

Rudanin Nikodimus ya bayyana fili a tattaunawarsa da Yesu. Bayan Yesu ya gaya masa, “ba wanda zai iya ganin mulkin Allah sai an sāke haihuwarsa.” (Yohanna 3:3), Nikodimus ya kalli Yesu ya ce,

“Yaya za a haifi mutum sa’ad da ya tsufa? Tabbatacce ba zai sāke koma sau na biyu a cikin mahaifiyarsa don a haife shi kuma ba!” (st. 4). Ma’ana, ya ce, “Yesu, me kake magana a kai?” Na gaskanta cewa wannan yana ɗaya daga cikin maganganu mafi rashin azanci da aka taɓa yi wa Yesu. A bayyane yake cewa Nikodimus ya rasa ainihin ma’anar abin da Yesu yake nufi.

Yesu yana magana ne game da sake haihuwa. Lura da Karin harafi a farkon kalma, *re*, wanda yake nufin “sake.” Kalmar nan *halitta* tana nufin “zama” ko “faruwa” ne a zahiri. Saboda haka, Yesu yana cewa dole ne wani abu ya “sake faruwa.” Sai dai kuma, ba haihuwar jiki yake nufi ba, amma haihuwa ta ruhu. Sabuwar haihuwa haihuwa ce ta gaske, amma haihuwa ce ta wani nau’i daban.

Domin amsa tambayoyin Nikodimus, Yesu ya fara bayyana wannan asiri. Ya ce, “Jiki yakan haifi jiki, amma Ruhu yana haifi ruhu” (st. 6). Yesu yana bayyana wata ma’ana ce a bayyane, wata tabbatacciyar gaskiya mai sauƙi, amma wadda Nikodimus yake buƙatar ya sake ji. Domin kuwa, yawancin ƙwararrun masanan tauhidi suna ɓata ne ba a kan wani babban sashi na ilimin tauhidi ba, amma a kan wani ginshiki na asali, wato gaskiya mai sauƙi wadda ya kamata su riga sun ƙware a kanta. A gaskiya ma, daga baya a cikin wannan tattaunawa, Yesu ya tsawata wa Nikodimus cikin sanyi-sanyi, yana cewa, “Kai ma da kake malami na Isra’ila, ba ka fahimci waɗannan abubuwa ba?” (st. 10). Kamar dai Yesu yana cewa ne: “Kunya ta tabbata

a gare ka. Ya kamata ka san waɗannan abubuwa. Ba ƙaga su nake yi ba. Waɗannan su ne matakan farko na sanin addini bisa ga Littafi Mai Tsarki."

Sabuwar haihuwa tana da matuƙar muhimmanci domin abin da aka haifa daga jiki, jiki ne—kuma ba za ka iya samun ruhu daga jiki ba. Idan kana son ka shuka bishiyar oak, dole ne ka shuka ƙwayar oak, ba wai strawberry ba. Jiki yana haifar da jiki kawai. Amma abin da aka haifa daga Ruhu, ruhu ne.

Don haka, Yesu yana yi wa Nikodimus magana ne game da sake haihuwa ta ruhaniya, ba wai kawai maimaita tsarin halitta na jiki ba. Wannan wani abu ne mai cike da asiri sosai.

Bayan Ya tabbatar da cewa yana magana ne game da abubuwa na ruhaniya, Yesu ya ƙara da cewa, "Kada ka yi mamaki da na ce, 'Dole ne a sāke haifarku." (st. 7). Idan akwai wani umurni da Yesu na Nazarat ya bayar wanda mutane suka yi watsi da shi, to wannan ne. Har yanzu mutane suna mamaki, suna farga-ba, kuma suna jin tsoro lokacin da wani ya ba da shawarar cewa ya zama dole a sake haifarsu. Amma Yesu ya ce: "Kada ku yi mamakin wannan. Kada ku yi al'ajabin wannan."

Sannan Yesu ya fara amsa tambayar Nikodimus game da "yadda" hakan yake faruwa. Amma yayin da yake bayyana wannan asiri, Yesu ma ya ƙara zurfafa shi ne. Ya ce: "ska takan hura zuwa inda take so. Kai kakan ji motsinta, sai dai ba ka iya sanin inda take fitowa ko kuwa inda za ta.

Haka yake ga duk wanda aka haifa ta wurin Ruhu." (st. 8). Akwai wani *wasan magana* mai ban mamaki a nan. Kalmar Helenanci *pneuma* ana iya fassara ta da "ruhu," "numfashi," ko "iska." Don haka, sa'ad da Yesu ya ce, "Dole ne a sake haifarku ta Ruhu, kuma yana kama da iska," yana nufin cewa *pneuma yana kama* da *pneuma ne*. Irin wannan wasan magana ya bayyana a cikin bayanin Yohanna game da abin da ya faru a dakin sama, sa'ad da Yesu ya hura wa almajiransa numfashi kuma ya ce musu, "Ku karbi Ruhu Mai Tsarki" (Yohanna 20:22). Kalmar nan da aka fassara a matsayin "hura numfashi" da kuma "Ruhu" ita ce *pneuma*. Yesu ya "pneumatized" (ya hura wa) almajiransa numfashi sannan ya ce, "Ku karbi *Pneuma* Mai Tsarki."

Yesu ya ce a takaice: "Nikodimus, kana so ka san yadda sake haihuwa ta ruhu take *faruwa? Pneuma* (Ruhu), wato Ruhu, yana busawa inda yake so. Yana kama da iska, yana busawa duk inda ya ga dama. Ba za ka iya ganinsa ba, amma za ka *iya* ganin tasirinsa. Haka *Pneuma* yake." Ma'ana, aikin sake haihuwa na Ruhu Mai Tsarki asiri ne.

Sabon Haihuwa Ba A Iya Gani Da Ido

A mataki mai sauƙi, aikin Ruhu asiri ne domin akwai tarin asirai da ke tattare da Ruhu Mai Tsarki da kansa. Ɗaya daga cikin manyan littattafan da aka taɓa rubutawa a tarihin ikklisiya game da mutuntakar da kuma aikin Ruhu Mai Tsarki shi ne wanda Abraham Kuyper ya rubuta,

wani masanin tauhidi wanda kuma ya yi aiki a matsayin Firayim ministan ƙasar Netherlands. A cikin gabatarwar shahararren littafinsa mai suna Aikin Ruhu Mai Tsarki, Kuyper ya rubuta:

> Ana iya ganin Kristi kuma ana iya jin muryarsa; a dā har hannuwan mutane sun taɓa Maganar Rai. Amma Ruhu Mai Tsarki ya bambanta kwarai. Game da Shi, babu abin da yake bayyana a siffar da ake iya gani; ba ya taɓa fitowa daga fagen da ba a iya gani ko taɓawa. Ta shawagi, ba tare da siffantuwa ba, kuma ba tare da siffar da za a iya fahimta ba, Ya kasance asiri. Shi kamar iska ne! Muna jin sautinta, amma ba za mu iya faɗar inda ta fito ba ko inda za ta tafi. Ido ba zai iya ganinsa ba, kunne ba zai iya jinsa ba, balle kuma hannu ya taɓa shi. Hakika, akwai alamu na nuni da bayyanar abubuwa: kurciya, harsunan wuta, karar iska mai ƙarfi, busawa daga tsarkakan laɓɓan Yesu, ɗora hannu, da yin magana da harsuna baƙi. Amma daga dukan waɗannan babu abin da ya rage; babu abin da ya ragu a baya, ko da kuwa ko da sawun ƙafa ɗaya ne.[1]

A takaice, Ruhu asiri ne saboda ba a ganinsa, kuma aikinsa na Sabon Haifuwa Asiri Ne saboda wannan dalili ɗaya. Babu wanda zai iya ganin abin da Allah yake yi a cikin ran wani. Shi ya sa aka gargaɗe mu a cikin Nassosi cewa yayin da mutum

1. Abraham Kuyper, *Aikin Ruhu Mai Tsarki (London: Funk &Wagnalls, 1900), 6.*

yake kallon Allah kuwa yana kallon zuciya ne (1 Sam. 16:7). Sake haihuwa gaskiya ce ta ruhaniya da take faruwa a cikin mutum, tana canza wannan mutumin, amma ba a ganinta, kamar iska ne.

Yayin da sake haifuwa ba abin ganuwa ba ne sake haihuwa, muna bukatar mu lura cewa Yesu ya ce za mu iya ganin sakamakonsa, kamar yadda muke gani, ji, da kuma jin sakamakon iska. Ina ne za mu duba don ganin bayyanannun shaidun sake haihuwa? Muna ganinsa a cikin 'ya'yan rayuwa da aka canza.

Dukanmu muna kokawa yayin da muke tantance rayuwarmu ta Kiristanci. Za mu iya ganin canje-canje a cikin rayuwarmu don alheri, amma kuma muna ganin abubuwan da ba mu so mu gani—abubuwan da ba mu so kowa ya gani. Don haka yayin da muke nazarin yanayin rayukanmu, muna bukatar mu tambaya ba inda muke ba sa'ad da aka sake haihuwarmu ko ma yadda hakan ya faru. Maimakon haka, muna bukatar mu tambaya ko akwai wata shaida ta canji a cikin canjin zuciyar mu da halinmu na ciki, da kuma halayenmu game da al'amuran Allah.

Mutanen da ba a sabunta sub a, a mafi kyau, bas u damu da abubuwan Allah ba. Mafi yawancin lokuta ma, suna nuna gaba a fili gare Shi. To, wasu na iya zama kamar suna neman Allah, amma Romawa 3:11 ta gaya mana cewa ba haka ba ne. Mutumin da ba a sake haifa ba ba ya taɓa neman Allah; shi mai gudu ne daga gaban Allah ne daga Allah. Yesu ya zo ne domin ya nema kuma ya ceci batattu (Luka 19:10). Shi ne Mai

Neman; mu ne kuma wadanda muke gudu. Wadanda ba a sake haifa ba suna neman farin ciki, kwanciyar hankali, sauƙi daga jin laifi, ma'anar rayuwa, da sauran abubuwa masu yawa wadanda muka sani Allah kadai ne zai iya ba su. Amma ba sa neman Allah. Suna neman albarkun Allah ne. Zunubin mutum na halitta dai shi ne: Yana son albarkun Allah ba tare da Allah da kansa ba.

Amma lokacin da Ruhu Mai Tsarki ya yi aikinsa na ban al'ajabi na sake haifuwa, abu na farko da yake canjawa a cikin mutum shi ne yanayin ransa. Yanzu sai ya fara kula da al'amuran Allah kuma yana da muradin neman Allah. Yanzu akwai wata soyayya ga Allah wadda ba ta nan a dā. Wannan canji bai zama cikakke ba tukuna, amma na gaske ne. Tushensa da ikonsa sun kasance abin ban al'ajabi. Amma gaskiyar ita ce zuciyar mutumin tana bugawa don Allah ne, alhali ba ta taɓa yin hakan ba a dā. Wannan shi ne sakamakon da ba za a iya musu ba na hurawar Ruhu ta cikin ran mutum.

Sabon Haihuwa Ita Ce Mafari

Sabon haihuwa shi ne mataki na farko a cikin dukkan halin fansa wadda Allah yake bi da mu ta cikinsa. Lokacin da mutane suka ce an sake haihuwarsu, sau da yawa suna tunanin cewa sake haihuwarsu abu ɗaya ne da sabuwar rayuwarsu. Domin kuwa, Sabon Alkawari ya ce mutumin da yake cikin Almasihu sabuwar halitta ne: "Saboda haka, duk wanda yake cikin Kiristi, sabuwar halitta ce, tsohon al'amari ya shuɗe, sabon ya zo!" (2 Kor. 5:17). Kasancewar mutum sabon mutum ne, wato sabuwar halitta, yana nufin cewa yana da sabuwar rayuwa, amma sabuwar rayuwarsa ba abu ɗaya ba ne da sake haihuwarsa. Maimakon haka, sabuwar rayuwarsa sakamakon sake haihuwarsa ne, kamar yadda kowace rana ta rayuwarsa take sakamakon haihuwarsa ta zahiri. Kowannenmu yana da ranar haihuwa a kowace shekara, amma ba a haihuwarmu a kowace shekara ba. Haihuwa sau ɗaya take faruwa, kuma tana nuna farkon kasancewar mutum a matsayin mutum a wannan duniya. Don haka, muna rarrabewa tsakanin farkon da kuma

rayuwar da take gudana daga wannan farkon, duka biyun ta fuskar haihuwa ta zahiri da kuma game da haihuwa ta ruhaniya, wadda ita ce abin da muke siffantawa da kalmar nan sake *haihuwa*.

Lokacin da na zama Kirista, na iske cewa na gamsu sosai da 2 Korintiyawa 5:17. Ina ɗaya daga cikin mutanen nan waɗanda suka fuskanci juyowa zuwa ga Allah farat ɗaya kuma cikin ban mamaki. A cikin watanni biyu na farko na kwarewata ta Kiristanci, rayuwata ta ruhaniya ta kasance kamar hawan jirgin sirdi mai saurin tashi da faɗuwa. Na tashi daga matuƙar farin ciki na ruhaniya zuwa matsananciyar damuwa ta ruhaniya. Ya yi kama da kwarewata game da wasan golf. Ban san sau nawa na faɗa wa matata ba: "Na samo shi. Na gano asirin. Ba zan sake buga mugun bugun golf ba. Ba zan sake samun zagaye marar kyau ba." Wannan yakan ɗauki kusan kwanaki biyu, sannan in sake fara nema ko'ina, domin nasara a wasan golf tana tafiya da sauri kamar yadda take zuwa. Haka kwarewata ta Kiristanci take a watanni biyu na farko. Na tashi daga kololuwar ruhaniya zuwa matsananciyar jin rashin kasancewar Allah, a lokacin da nake sake komawa cikin tsofaffin dabi'un zunubi.

Wannan ya ci gaba har sai da na nemi taimako daga wurin wani fasto wanda ya ba ni wannan shawara mai hikima: "Ka tuna cewa sake haihuwarka farko ne kawai. Sabon Alkawari ya ce ko da yake kana iya zama babban mutum ta kowane fanni (balaga, gogewa, ilimin boko), idan kwarewarka ta Kiristanci

sabon abu ne a to ta fuskar ruhaniya, kai jariri ne. Kana cikin matakin jariri."

Yi la'akari da yanayin motsin rai na jarirai. Shin ka taba lura da yadda suke saurin sauyawa? Jariri na iya kasancewa yana kuka da ƙarfi, amma idan ka ce masa, "Goo, goo, goo" kuma ka jawo hankalinsa ga wani abu dabam, sai ka ga farat ɗaya yana yin dariya. Amma bayan daƙiƙa goma, yana iya sake yin kuka. Motsin ran yaro yana kasancewa haka har sai ya kai ga matakin da tashin da faɗuwar ba sa kasancewa da tsanani sosai. Haka nan ma, a cikin girman ruhaniya, muna bin wani yanayi na ci gaba da ke ƙaruwa inda tashinmu da faɗuwarmu, bayan wani lokaci, suna rage tsanani. Yayin da muke girma a cikin balaga, muna samun daidaituwa a cikin yanayin halayenmu na ruhaniya.

Amma sake haihuwa farkon mataki ne kawai na wannan tsari da yake ci gaba har sai an ɗaukaka mu a Sama. Gwagwarmayar tana ci gaba tun daga ranar sake haihuwa har zuwa wannan ranar a sama lokacin da za mu kai ga cikar balaga a cikin Almasihu.

Ina jin haushi sa'ad da na ji masu wa'azi masu kyakkyawan nufi, a ƙoƙarinsu na shawo kan mutane game da wadatar imanin Kirista, suna cewa, "Zo wurin Yesu kuma dukan matsalolinka za su ƙare." Wannan sam ba gaskiya ba ne. Rayuwata ba ta fara zama mai sarkakiya ba sai da na zama Kirista, domin a sannan ne kawai ya zama dole in shiga yaƙi a kowace rana tsakanin abin da yake na jiki da kuma abin da yake na Ruhu.

Rikicin a ci gaba yake saboda iyawar yin mugunta da take zaune a cikin zuciyar mutumin da aka sake haifa kusan ba ta da iyaka. Bai kamata mu yi mamaki da yawa ba sa'ad da muka ga shugabannin Kirista suna faɗawa cikin zunubi mai tsanani. Muna da ikon sabuwar rayuwa, amma hakan ba ya share tsoffin ɗabi'unmu na kafin tuba kai tsaye (duba Gal. 5:16–26; Rom. 6–7). Sake haihuwa farkon mataki ne kawai. Amma ba wai kawai farkon mataki ba ne—shi ne ainihin mafarin. Shi ne mafari mafi mahimmanci da za ku taɓa samu.

Mun Taɓa Zama Matattu

Ina so in ja hankalinku zuwa ga wasu muhimman abubuwa game da farkon rayuwar Kirista. Muna bukatar mu ga daga me aka sake haifarmu. A farkon babi na biyu na wasiƙarsa zuwa ga Afisawa, Bulus ya rubuta: "Kuma ku matattu kuke a cikin laifofinku da zunubanku waɗanda kuka yi tafiya a cikinsu dā, kuna bin hanyar wannan duniya" (st. 1–2a).

Dukanmu muna da dabi'u. Dukanmu muna da ra'ayi, wato yadda muke kallon duniya da kuma yadda muke kallon kanmu. Dukanmu muna da abubuwan da muka fi so. Muna ƙoƙarin yin rayuwa bisa ga wani irin mizanin ko ma'auni jagora. Ta yaya kake yin rayuwarka? Menene mizaninka? Daga ina ka same shi? Mafi mahimmanci ma, me ya sa ya zama mizaninka?

Manzon ya bayyana a nan cewa, "Kafin a sake haifarku, kun kasance matattu." Babu shakka ba maganar mutuwar jiki yake yi ba.

Wannan saƙon, wannan wasiƙar, ba a aika ta zuwa gidan ajiyar gawa ba ne. Tana zuwa ne ga mutanen da suke raye a jiki. Bulus yana cewa Afisawa, da kuma mu kanmu, a dā matattu ne a ruhanceMu matattun mutane ne masu tafiya—wato rayayyun matattu. Muna raye a jiki amma matattu ne a ruhance.

Ta yaya muka yi tafiya? Bulus ya ce mun yi tafiya bisa ga “hanyar wannan duniya.” Idan ka shiga gasa tsere tare da wasu yan wasa dari biyar, sai ka yanke shawarar barin sawun ka yi naka tseren, ba za ka sami kyautar ba duk da yadda ka yi sauri, saboda ba ka tsaya a cikin iyakokin gasar – cikin hanyar da aka tsara don gudu ba. Akwai takamaiman hanyar tseren da ya kamata masu gudu su bi. Bulus yana cewa kafin a sake haifarku, kun yi rayuwarku ne bisa ga yanayin da wannan duniya ta gindaya muku.

Mu mutane kan yi kama da bayi wajen bin tsari dabi’u da kima na abokanmu, musamman a lokacin da muke matasa. Matasa sukan fi karkata ga lura da abokan zamansu. Furucinsu na yau da kullum shi ne, “Kowa yana yin hakan.” Sukan rasa barci da dare saboda damuwar ko suna tafiya da zamani game da sabbin abubuwa da ado da yayi. Amma, ko shakka babu, a ƙarshen shekarun matasan muna daina hakan, ko ba haka ba? Kun san ba haka ba ne. Muna karkata ga ci gaba da lura da iyakokin tsarin tafiyar wannan duniya. Bulus ya ce wannan bautar bin yanayin da duniya ta gindaya mana ita ce alamar mutumin da ba a sake haifarsa ba.

Ba wannan kawai ba, Bulus ya ce, mun yi rayuwa ne bisa ga “kuna biyayya ga sarki masu ikon sarari sama, wato, ruhun nan da yanzu yake aiki a cikin masu ƙin biyayya ga Allah. Dukanmu a dā mun yi irin rayuwan nan a cikinsu, muna bin kwaɗayi da sha’awace-sha’awacen jikunanmu da tunaninmu. Kamar sauran mutane, mun cancanci fushin Allah.” (ayoyi 2b–3).

Wannan yana ɗaya daga cikin mafi bayyanannun kwatanci da cikakken bayanin halin mataccen rai, da kasala, da rashin rai na mutumin da ba a sake haifarsa ba wanda muke samu a cikin dukkan Littafi Mai Tsarki. Waɗanda ba a sake haifarsu ba suna ƙarƙashin tasirin maƙiyi kuma suna neman biyan sha’ace-sha’acen jiki da muradin jiki da na hankali. Wannan ba bayanin salon rayuwar manyan masu laifi ba ne kawai ko kuma masu neman jin daɗin duniya na haƙiƙa. Wannan ita ce hanyar da kowa yake rayuwa, ba tare da togaciya ba. Dukkan duniya tana rayuwa ne a al’adance kuma a dabi’ance bisa ga wannan tafarki na faɗuwar dabi’ar mutum.

Amma Allah . . .

Dukkan wannan bayanin ya mayar da hankali ne a kan hali kafin sake haifuwa. Kalma ta gaba a cikin Afisawa 2 ita ce take kai mu ga sake haifuwa. Kalma ce da take burge ni ƙwarai, domin tana ƙunshe da kuma tattare dukkan saƙon fansa: amma. Bulus *ya* rubuta, “Amma saboda yawan ƙaunar da yake mana, Allah, wanda yake mai yawan jinƙai, ya ba mu rai sa’ad da ya tashe Kiristi daga

matattu. Ta wurin alherin Allah ne aka cece ku." (aya 4–5).

Bulus ya yi amfani da wata kalma mai ɗan wuyar fahimta a nan don ya yi *nuni* ga sake haifuwa: raya. A cikin Nassosi, raya abu ba yana nufin sa shi ya yi sauri ba ne. Yana nufin sa wannan abun ya kasance da rai ne. Muna faɗa a cikin Shaidar Bangaskiya ta Manzanni cewa sa'ad da Yesu zai dawo zai shari'anci "masu-rai da matattu." Ba a ce masu sauri da masu nauyi ba. Bambancin yana tsakanin waɗanda suke da rai da waɗanda suke matattu, kuma wannan shi ne bambancin da manzon yake zana mana a nan cikin Afisawa. A dā muna matattu a ruhu, amma Allah ya raya mu. Ya sa mu kasance da rai. Ya fitar da mu daga yanayin mutuwa. Tsarin nan da ya yi amfani da shi don yin hakan shi ne sake haifuwa. Shi ne farkon sabuwar rayuwa.

Bugu da ƙari, sake haifuwa wani abu ne da Allah ne kaɗai ke aiwatar da shi. Matattu ba zai iya tada kansa daga mutuwa ba. Iko ɗaya tilo a sararin samaniya wanda ke da iko bisa mutuwa shi ne ikon Allah. Allah ne kaɗai zai iya fito da wani abu daga babu, kuma ya fito da rai daga mutuwa. Mataccen mutum ba zai iya yin komai ba ban da ya ci gaba da kasancewa mataccе. Rayar da mu, wato matakin farko da ya shigar da mu cikin sabuwar rayuwa gaba ɗaya kuma ya mayar da mu sababbin halittu, an aiwatar da shi ne ta wurin aikin Allah Maɗaukaki.

Akwai wasu kalmomi guda biyu waɗanda ba sa cikin harshenmu na yau da kullum na Kiristoci, amma suna da muhimmanci

ƙwarai don fahimtar aikin Allah a cikin sake haifuwa. *Kalmomin* su ne monergism (aikin *gefe ɗaya*) da kuma synergism (aikin haɗin gwiwa). Bari in rarrabe muku waɗannan kalmomi don in taimaka muku ku ga abin da suke nufi. Ƙarin *harafin* nan mon yana nufin "ɗaya"—wani abu da yake shi kaɗai ne. Erg kuma ma'aunin aiki ne ko na aiki. Mun sami kalmar *makamashi* (energy) ne daga wannan asalin. Don haka idan muka haɗa su duka, monergism yana nufin, a zahiri, "mutum ɗaya ne ke aiki." Aikin monergistic shi ne wanda ɓangare ɗaya ne kawai yake aiwatar da aikin. Ƙarin harafin nan syn yana nufin "tare da" ko "tare." Don haka aikin synergistic (aikin haɗin gwiwa) shi ne wanda mutum biyu ko fiye da haka suke aiki tare don kammala wani aiki. Aikin synergistic aiki ne na haɗin gwiwa.

Yaya wannan ya shafi ilimin tauhidi da kuma tattaunawarmu game da sake haifuwa? Sake haifuwa ta ruhaniya aikin monergistic ne (aikin gefe ɗaya), ba aikin synergistic (aikin haɗin gwiwa) ba. Allah ne kaɗai yake aiwatar da sake haifuwa. Kamar yadda na ambata a sama, matacce ba zai iya ba da haɗin kai a cikin tashiwarsa daga matattu ba. Yesu bai je kabarin Li'azaru ya ce: "Li'azaru, ina buƙatar ka taimake ni mu shawo kan mummunan sakamakon mutuwarka kwanan nan" ba. Ba haka ya yi magana da Li'azaru ba. Li'azaru ya kasance maras taimako kuma maras bege domin ya mutu. Maido da mutum daga mutuwa ta ruhaniya zuwa rai na ruhaniya abu ne da Allah kaɗai zai iya yi.

Bayan Allah ya raya mu, sa'an nan dole ne mu shiga ciki. Dole ne mu yi imani, mu tuba, kuma mu bidi abubuwan Allah. Amma kafin Allah ya raya mu, ba za mu iya yin wadannan abubuwan ba. Muna bukatar Allah ya dauki matakin farko don ya canza yanayin zukatanmu, yana raya rayukanmu domin mu iya ba da amsa ta hanyar rungumar Kristi da kuma gudu zuwa gare Shi cikin tuba.

Abin nufi a nan shi ne, matakin farko daga Allah yake. Ceto na Ubangiji ne. Idan kwanan nan ka zama Kirista, kuma kana kokarin fahimtar abin da ya faru da kai, ina tsammanin yana da matukar muhimmanci ka fahimci wannan gaba tun da wuri a cikin girmanka na Kirista, domin ka sami cikakkiyar godiya ga alherin Allah wanda aka kafa tun farkon tafiyarka da Shi.

Allah Ne Ke Aiwatar da Sabon Haihuwa

Wani lokaci can baya, an bukace ni da in yi jawabi a wurin wani taron maza a Jackson, Mississippi. Yayin da ranar ziyarar tawa ta kusanto, masu daukar nauyin taron suka sanar da ni cewa abin da suke bukata daga gare ni ba jawabin koyarwa na yau da kullum ba ne, said ai sakon bishara. Bayan sakon kuma, za a yi kiran mutane su ba da kansu ga Kristi. Idan har akwai wani mai jawabi da ya taba cika da matsananciyar farga-ba da tsoro, to ni ne lokacin da na sami wannan sanarwar. Ina da matukar girmamawa ga wadanda Allah yake amfani da su a matsayin masu bishara, amma ni malami ne, ba mai bishara ba.

Na kira su, na kuma gaya musu cewa sun sami mutumin da bai dace ba. Na gaya musu cewa Allah yana sa albarka a koyarwata, amma duk lokacin da na yi ƙoƙarin yin bishara don kira zuwa ga tuba, ba wanda yake amsawa da gaske. Kamar dai Allah yana yi mini rada ne yana cewa, “Kai, wannan ai ba baiwarka ba ce.” Amma suka ƙi yarda da hakan.

Don haka na yi huɗuba a wurin taron kuma na yi kiran mika wuya ga Kristi. Ba a samu amsar dubban mutane ba, amma abin mamaki, wasu maza sun mika rayuwarsu ga Kristi a karon farko. Bayan haka, na zauna da mutanen da suka shirya taron kuma na ce: “Shin kun fahimci abin da ya faru a nan? Yayin da muke cikin taron ’yan Adam, kuma yayin da nake magana da karatu daga cikin Littafi Mai Tsarki, Mahaliccin dukan sararin samaniya ya shigo cikin dakin nan kuma a asirce, ta hanyar da ba a gani ba, cikin hanyar asiri, kuma ta ikon Allah, ya canza rayukan mutanen da ke nan.” Na gaya musu: “Wannan ya faru. Kuma Allah ne ya yi shi.”

A wannan dare, waɗannan mutanen da suka amsa bishara, har zuwa matsayin da suka mallaki bangaskiyar da suka furta, an canza su a can cikin zurfin rayukansu. An karkatar da su daga tafarkin duniya zuwa wani sabon tafarki, wato tafarkin rayuwar Kirista. Ga waɗanda aka sake haifarsu ta ruhaniya ta wurin Ruhu Mai Tsarki a wannan dare, wancan taro ya zama sabon mafari ne. Haka yake ga dukan waɗanda suka fuskanci sabuwar haihuwa—ita ce farkon rayuwar Kirista.

Sabon Haihuwa Aikin Allah Ne Mai Cikaken Iko

Ga wata tsarin tauhidi da za ta iya ba ku mamaki: “Sake haihuwa tana riga bangaskiya.” Mun gani cewa sake haihuwa, ko kuma sake haihuwa ta ruhu, ita ce farkon rayuwar Kirista. Idan sake haihuwa ita ce mataki na farko, a bayyane yake cewa lallai sai ta riga mataki na biyu. Mutanen da suka mutu a ruhance ba sa hanzarin samun bangaskiya farat ɗaya, wanda zai sa Allah ya sake haifarsu. Maimakon haka, bangaskiya ita ce amfanin sake haihuwar da Allah yake aikatawa a cikin zukatanmu: “Ko sa'ad da muke matattu cikin laifofinmu, [Allah] ya raye mu tare da Almasihu” (Afis. 2:4b). An sake haifarmu (sake haihuwa), sannan mu zo ga bangaskiya, sannan a barata da mu, sannan mu fara bi ta tsarin tsarkakewa na tsawon rai (Rom. 8:30). Dukkan waɗannan abubuwan sun haɗa daukacin sarkakiyar rayuwar Kirista. Amma mafarar, mataki na farko a cikin jerin, gaba ɗayansa na Allah ne—aiki ne na nufin Allah shi kaɗai, kamar yadda muka gani a babi na baya.

A takaice, sake haihuwa aiki ne na mulkin Allah. Ma'ana, Allah yana amfani da ikonsa da kuma ikon ikonsa a kanku a lokacinsa da kuma yadda ya so domin ya kawo sake haihuwar zuciyarku. Na nanata wannan ne domin mutane da yawa suna fahimtar sake haihuwa a matsayin kawai wani aiki na rarrashin ɗabi'a inda Allah yake lallashinmu ko jan hankalinmu mu canza kuma mu zo ta hanyarsa. Abin da nake nufi shi ne, bin tunanin Augustine da sauran manyan magabatan bangaskiyar Kirista, cewa sake haihuwa ba wai Allah yana tsaye ne a gefenmu yana ƙoƙarin shawo kanmu mu zo gare shi ba, amma Allah ne yake shigowa cikinmu. Yana mamaye kurwa, domin lallai sai an sami babban canji a zuciya kafin mu iya zuwa ga Almasihu. Domin mu yi sha'awar abubuwan Allah, lallai sai an raye mu, kuma domin a raye mu ana buƙatar aikin ikon mallaka na Allah..

Bayahude na Gaske

A cikin Ayyukan Manzanni 9, muna da labari mafi shahara na tuba a tarihin ikklisiya. Shi ne tubar Shawulu, mutumin da ya zama manzo Bulus. Sabon Alkawari yana koyarwa cewa ba masu hikima da manyan mutane da yawa ba ne Allah ya kira su zama sashe na tushen ikklisiya Kirista (1 Kor. 1:26–27). Maimakon haka, ikklisiya farko ta ƙunshi galibi waɗanda ake zalunta, matalauta, waɗanda ake amfani da su, da kuma waɗanda suke da ƙarancin abin hannu. Wannan sashe ne na shirin Allah, mafi yawanci, na kada ya zaɓi masu arziki, masu iko, da shahararru don kafa ikklisiyan sa.

Amma Nassosi ba su ce “ko guda ba” amma sun ce “ba da yawa ba” aka ɗauka daga matsayi na shugabanci ko manyan matakai na matsayi. Wanda ya fito daga irin wannan asali shi ne Shawulu na Tarsus.

Shawulu ya fito ne daga iyalin ‘yan kasuwa kuma ya sami babban ilimi na musamman. Wasu masana sun tabbatar da cewa idan har Shawulu bai haɗu da Kristi ba a kan hanyar Damascus kuma ya tuba kwarai da gaske, idan Allah ya bar shi ya ci gaba da bin tafarkin da yake kai, tabbas duniya ta zamani za ta san da shi, domin yana cikin Yahudawa waɗanda suka fi kowa ilimi a ƙarni na farko. Shi ne tauraron ɗalibi na Gamaliel, babban malamin addini na Yahudawa a Urushalima. Ya riga ya sami ilimi da ya yi daidai da digirin digirgir (PhD) guda biyu sa’ad da ya kai shekara ashirin da ɗaya. Sa’ad da yake saurayi, ya tashi cikin sauri irin na tauraro mai wutsiya zuwa matsayi na ikon siyasa, tauhidi, da na addini a Isra’ila.

Shawulu ba wai kawai masani ne kuma kwarewa ba, har ila yau yana da himma sosai. Shi mai kishin addini ne. Ya bayyana kansa a matsayin wanda yake “na kuma yi ƙwazo ƙwarai ga bin al’adun kakannina” (Gal. 1:14b) kuma a matsayin “Bayahude na gaske” (Filib. 3:5). Ba mu tabbata takamaiman abin da yake nufi da hakan ba, amma mun sani cewa yana siffanta kansa ne da mafificiyar kalma a harshen Yahudawa, makamanciyar kalmomin nan “Sarkin sarakuna” ko “Ubangijin iyayengiji.” Ma’ana, Shawulu

mutum ne na dabam. Ya kai matsayi mafi daukaka da za a iya kaiwa.

Shawulu kuma ya kasance Bafarisi ne (Filib. 3:5), memba a rukunin masu ra'ayin mazan jiya na shugabannin Yahudawa waɗanda suka himmatu wajen kiyaye dokar Musa daki-daki. Wata al'ada daga zamani ikklisiya ta farko tana nuna cewa a cikin Farisiyawa akwai wata kungiya ta ciki da ta yi imani cewa idan dayansu zai iya kiyaye dukan dokoki iri-iri da suka sadaukar da kansu gare su daidai na rana daya kacal, wannan aikin nagarta zai sa Allah ya aiko da Almasihu. Don haka akwai wasu tsirarun masu kishin addini a cikin Farisawa waɗanda suka yi kowane irin horon kai da guje wa jin daɗin duniya. Sun kasance masu ibada sosai a cikin karatunsu, kuma suna kula da kowane karamin daki-daki na dokar sosai, a kokarinsu na kiyaye ta daidai ta sa'o'i ashirin da hudu. Wasu suna hasashen cewa Shawulukansa yana ɗaya daga cikin waɗannan Farisawa masu kishin addini.

Mun haɗu da Shawulu a karon farko sa'ad da yake riƙe da rigunan waɗanda suke jifan Isitifanus (Ayukan Manzanni 7:58). A cikin Ayukan Manzanni sura ta 8 da ta 9, muna ganin ya mayar da kishinsa ya zama wani nau'i na ƙiyayya mai tsanani ga ikklisiya da ke tasowa, wadda yake ɗauka a matsayin gurbataccen sigar addinin Yahudanci na asali. Yana kallon harkar Kiristanci ba a matsayin cikar Nassosin Tsohon Alkawari ba, amma a matsayin abin da ke lalata duk wani abu da yake ƙauna. Don haka Shawulu ya yi aiki

tare da shugabannin addinin Yahudawa don gabatar da tuhuma a hukumance ga Kiristoci. Ya cika da ƙiyayya ga Yesu da duk abin da Yesu yake wakilta.

Almasihu Ya Fuskanci Shawulu

Amma komai ya canza a cikin Ayukan Manzanni sura ta 9, wadda ta buɗe da wadannan kalmomi: "Ana cikin haka, Shawulu ya ɗage yana barazana yin kisa da tsananta wa almajiran Ubangiji. Sai ya je wurin babban firist ya roƙe shi ya ba shi wasiƙu zuwa majami'un Damaskus, don in ya sami wani a wurin wanda yake bin wannan Hanya, ko maza ko mata, yă kama su a matsayin 'yan kurkuku yă kai Urushalima." (st. 1–2). Kowane numfashi da Shawulu yake fitarwa yana fitar da wata irin barazana ta shaiɗanci ne ga rayukan masu bi, kuma ba kawai wadanda ke Urushalima ba. Ya tambayi babban firist wasiƙun goyon baya na hukuma domin ya ci gaba da bincikensa, da gurfanarwa, da kuma tsananta wa Kiristoci a Damasƙus. Ya so ya tafi har Damasƙus don ya nemo kowane Bayahude da ƙila ya kamu da wannan bidi'a ta Kiristanci. Wannan yana kama da jami'in ɗansanda ne da ya tafi wurin alkali don ya karɓi sammacin kotu. Shawulu ya so ya farauci Kiristoci, maza da mata, ya kuma kawo su a ɗaure da sarƙoƙi zuwa Urushalima.

Amma Shawulu bai taba cika nufin aikinsa a Damasƙus ba: "Da ya yi kusa da Damaskus a kan hanyarsa, ba zato ba tsammani sai wani haske daga sama ya haskaka kewaye da shi. Sai ya fãdî a ƙasa ya kuma ji wata murya ta ce masa, "Shawulu,

Shawulu, don me kake tsananta mini?" Shawulu ya yi tambaya ya ce, "Wane ne kai, ya Ubangiji?" Ya amsa ya ce, "Ni ne Yesu wanda kake tsananta wa. Yanzu ka tashi ka shiga cikin birnin, za a kuma gaya maka abin da dole za ka yi."" (aya ta 3–6).

Idan har akwai wata shaida a cikin Nassosi cewa sabon haihuwa aiki ne na Allah mai cikakken iko, wannan shi ne. Shawulu bai yi kome da ya cancanci wannan shiga tsakani na banmamaki a rayuwarsa ba. Babu wani cancantaccen aiki a cikin aikinsa ko rayuwarsa da zai iya sa Allah ya aiko da wannan ziyara ta alheri; hakika, akwai ma rashin cancanta mai girma. Duk da haka, Yesu ya zo wurin Shawulu, kuma aka juyar da Shawulu ta ikon Allah, yadda aka samu sakamako a nan take.

Daga baya, yayin da yake rubutu a matsayin manzo Bulus, ya tuna cewa Yesu kuma ya ce, "Yana da wuya ka shuri tsinken tsokanar dabba." (Ayyukan Manzanni 26:14). Wannan wani baƙon hoto ne. A duniyar dā, sa'ad da ake amfani da shanu don jan amalanke, wani lokaci shanun kan taurare, kamar alfadarai, sai matuƙin ya daki bayansu da bulala don su ci gaba da tafiya. Wani lokaci kuma, sa'ad da shanun suka ƙi motsawa kwata-kwata kuma suka ji zafin bulalar, sai su shilla ƙafafunsu na baya su yi duka, wataƙila har su farfasa amalanken. Saboda haka mutane suka fara sanya hantsar shanu a gaban amalankensu. A jikin hantsar, akwai wasu ƙaya masu ƙarfi da kaifi waɗanda za su ji wa kofatun shanun rauni kuma su hana su shuri. Amma wani lokaci san da yake da

wauta sosai yakan “yi shurin hantsar.” Zafin da yake ji daga dukan hantsar sau ɗaya zai sa san ya ƙara fusata, sai ya sake yin duka da ƙarfi fiye da dā. Idan ya ci gaba da dukan, zai ƙara jin zafi, idan ya ƙara jin zafi, zai ƙara yin fushi, idan ya ƙara yin fushi kuwa, zai ci gaba da dukan. San zai ruda kansa da jini yayin da yake faɗa da hantsar.

Yesu yana cewa: “Shawulu, kai wawan sa ne. Me ya sa kake tsananta Mini? Ba za ka iya yin nasara ba. Kana kama da sa da yake dukan ƙayoyin hantsar.”

Yayin da Shawulu yake kwance a ƙasa, ya duba sama cikin haske mai ƙyalli ya tambaya, “Wane ne kai, Ubangiji?” Bai san wanda ya tsayar da shi a kan hanyarsa ba, amma ya san cewa lallai Ubangiji ne, gama babu wani da zai iya haskaka hamada a tsakiyar rana da haske mai ruruwa na ɗaukaka mai haske ƙwarai. Babu wani da zai iya kada shi zuwa ƙasa kuma ya makantar da shi. Babu wani kuma da zai iya yi masa magana da murya daga sama a cikin harshensa. Lallai Ubangiji ne yake yi masa magana. Yesu ya amsa: “Ni ne Yesu, wanda kake tsananta wa. Amma tashi ka shiga birnin, za a kuma gaya maka abin da za ka yi.”

Shin Allah Ya Fuskance Ka?

Wataƙila ba ka taɓa ganin haske mai ƙyalli a kan hanyar Damascus ba. Wataƙila ba a taɓa kaɗa ka zuwa ƙasa ba. Ina da yakinin cewa ba ka taɓa jin murya da ake ji da kunne daga

Sama ba. Game da yanayin Shawulu, waɗannan abubuwa bayyanannun ayyuka ne kawai na zahiri game da aikin asiri na sake haifuwa da yake faruwa a ciki. Amma wannan ikon Allah da iko da ka bayyana a kan hanyar Damascus a ranar nan ya kasance yana aiki a cikin ranka idan har haƙiƙa an sake haife ka.

Sake haifuwa aiki ne na ikon Allah Mai iko duka, ikon da babu abin da zai iya rinjaya ko ya bijire masa. Idan Allah ya hura wa mutum rai daga matattu, wannan mutumin zai dawo da rai daga matattu. Babu wata jayayya sa'ad da aka yi amfani da wannan ikon. Allah ta wurin ikon mulkinsa ya tunkari Shawulu, kuma ta wurin ikon mulkinsa ya canza shi, ya kuma fanshe shi. Shin ya yi maka hakan kuwa?

Sabon Haihuwa Tana Faruwa Nan Take

Lokacin da nake yaro ina wasa a waje, mahaifiyata takan kira ni ta hanyar cewa, “R.C., shigo ciki ka ci abinci.” Ta kan faɗi hakan sau biyu, amma daga nan, idan na yi jinkiri da yawa kuma na gwada haƙurinta, sai ta ce, “Saurayi, shigo cikin gidan nan nan *take,” tana* jaddada kowane gaɓa na kalmar. Lokacin da na ji haka, na san cewa ina buƙatar in shiga gidan ba tare da ɓata lokaci ba.

A fannin tauhidi, muna cewa sake haifuwa tana faruwa ne nan take. Ta hanyar faɗin haka, muna bayyana cewa sake haifuwa tana faruwa ne farat ɗaya; tana faruwa ne a take. Amma a wannan yanayin, ma’anar *kalmar nan* take ta wuce batun lokaci kawai. Faɗin cewa sake haifuwa tana faruwa nan take kuma yana nufin cewa tana faruwa ne ba tare da wasu hanyoyi ba, wato ba tare da wani sanadi ko tsaka-tsaki ba.

Sabon Haihuwa Tana Faruwa Nan Take

Na yi nuni a baya cewa na fuskanci tubar farat ɗaya. Wasu kuma, suna da abubuwan da suka faru na tuba sannu-sannu,

mai ɗaukar lokaci; ƙila ma ba su san shekarar da suka zama Kiristoci ba. Suna cewa: “Ban san lokacin da abin ya faru ba. Abu ne da ya faru sannu-sannu cikin shekaru da dama.” Ta yaya, to, zan iya tabbatar da cewa sake haifuwa tana faruwa ne farat ɗaya? Muhimmin abin fahimta yan cikin yadda na yi amfani da kalmar nan *abubuwan da suka faru na tuba*. Ina magana ne game da abin da muke sane da shi. Zan iya cewa sani na na zama Kirista ya kasance farat ɗaya ne, ba zato ba tsammani, kuma nan take. A gefe guda kuma, wani zai iya cewa, “Na dai samu fahimtar hakan ne sannu-sannu.” Don haka za mu iya bambancewa tsakanin masaniyar kanmu game da abin da Allah yake yi a cikinmu da kuma aikin kansa.

A shekara ta 1980, an yi wani fim mai *suna Crocodile Dundee* wanda ya biyo bayan abubuwan da suka faru na wani mutum daga yankin karkara na Ostareliya wanda ya zo Birnin New York. Lokacin da ya isa New York, wata ’yar jarida ta tarye shi tana tambaya, “Shekarunka nawa?” Ya ce, “Ban sani ba.” Ta ce: “Ba ka sani ba? Ta yaya ba za ka sani ba?” Ya amsa da cewa, “To, na tambayi sarkin ƙabilar da ya san ni sa’ad da aka haife ni. Sarkin ya ce, ‘A lokacin bazara.’” Don haka Crocodile Dundee bai san takamaiman lokacin da aka haife shi ba. Amma shin hakan yana nufin ba shi da ranar haihuwa? A’a, ko shakka babu. Akwai lokacin da yake ba a haife shi ba kuma akwai lokacin da aka haife shi, kuma canjin daga wani yanayi zuwa wani ya faru ne farat ɗaya (ko kusan haka). Kawai dai bai san lokacin da abin ya faru ba. Haka ma, akwai mutane da yawa

da ba su san lokacin da aka sake haifuwarsu ba.

Don haka mutum zai iya kasancewa bai sani ba ko yaushe ko kuma ta yaya aka sake haifuwarsa. Amma ba shi da muhimmanci ka san yaushe ko ta yaya ka zama Kirista. Abin da kawai yake da muhimmanci shi ne *shin* an sake haifuwarka. Wannan yanayi ne na lallai ɗaya daga cikin biyu. Ko dai ka kasance matacce a ruhance ko kuma kana raye ga al'amuran Allah. Ko dai kai wanda ba a sake haifuwarsa ba ne ko kuma wanda aka sake haifuwarsa. Babu wani yanayi na tsaka-tsaki. Kamar juna biyu ne; babu wanda yake kusan yana da juna biyu. Haka ma, babu wanda yake kusan samun sake haifuwa. Ko dai an yi ko kuma ba a yi ba.

Sake Haihuwa ba ta Zuwa ta Wurin wata Hanya

Don haka sake haifuwa tana faruwa ne nan take. Amma sa'ad da na ce sake haifuwa tana faruwa ba tare da wata hanya ba, ina nufin fiye da haka. Ina nufin cewa sa'ad da Allah ya ba ka rai na ruhaniya, ba ya amfani da wata hanya dabam ban da kansa domin yin hakan. Sa'ad da likita yake yi maka maganin wata cuta ta hanyar ba ka takardar magani, maganin shi ne hanyar da yake amfani da ita domin ya warkar da kai. Amma maganin rashin ran ruhaniya, wato sake haifuwa, ba a bayar da shi daki-daki. Babban Likitan nan yana warkarwa ne nan take.

Linjila bisa ga Markus ta haɗa da wani labari mai ban mamaki game da warkarwa da Yesu ya yi. Misali ne ba na warkarwa nan

take ba, amma na warkarwa wadda aka yi amfani da wata hanya. Mun karanta: “Suka iso Betsaida, sai waɗansu mutane suka kawo wani makaho, suka roƙi Yesu yă taɓa shi.” (8:22). Babu shakka wannan makaho yana da abokan da suka damu da shi, kuma tun da sun ji labarin ayyukan mu’ujiza na Yesu, sai suka yanke shawarar kai abokinsu gare Shi. Suna so su ga makahon ya amfana daga ikon Yesu na allahntaka.

Yesu ya yi wani abu mai ban mamaki: “Yesu ya kama hannun makahon ya kai shi bayan ƙauyen.” (st. 23a). Ka yi tunanin hakan. Yawanci wani zai zo wurin Yesu ya ce, “Yesu, Ɗan Dawuda, ka yi mini jinƙai,” kuma lokacin da Yesu ya ji haka, sai ya amsa: “Zan yi haka. Ka tafi lafiya.” Ma’ana, Yesu yakan warkar da mutumin ne kawai a take a wurin. Amma a wannan yanayin, Yesu ya fitar da mutumin daga taron jama’a domin warkarwarsa kada ta zama abin kallo ga jama’a. Bugu da ƙari, Yesu ya yi jagorancinsa ta hanyar kama *hannunsa*. Alheri bai taɓa kasancewa mai tausasawa fiye da wannan ba—Allah cikin jiki ya kama hannun makaho yana yi masa jagora zuwa wurin sirri domin warkarwa. Wane irin babban kulawa ne Yesu ya nuna ga mutuncin mutumin. Ina mamakin sau nawa abokai suka yi ta yawo da wannan mutumin. Ya dogara ga wasu don su yi masa jagora. Ka yi tunanin yadda ya kasance maras taimako a waɗancan yanayi. Amma yanzu Yesu Almasihu ne yake yi masa jagora. Bai taɓa samun jagora amintacce kamarsa ba a rayuwarsa.

Markus kuma ya ƙara da cewa: “[Ya fitar] Bayan ya tofa miyau a idanun mutumin, ya kuma dĩbiya masa hannuwansa, sai ya tambaye shi ya ce, “Kana iya ganin wani abu?”?’” (st. 23b). Na yi ƙoƙarin jaddada batun nan cewa Yesu ya yi iyakacin ƙoƙarinsa don ya kāre mutuncin wannan makaho. Duk da haka, da zarar Ya fitar da shi daga gaban taron jama’a masu kallo, sai Ya tofar da miyau a idanunsa. A al’adarmu, wannan zai zama alamar wulakanci ne da aka yi domin a ƙasƙantar da mutum. Amma a bayyane yake cewa hakan ba shi ne nufin Yesu ba. Lokacin da Yesu ya tofar da miyau a idanun makahon kuma ya ɗora masa hannuwansa, yana sadarwa da mutumin ne ta hanyar taɓawa.

Wannan labari yana kama da wani bayani a cikin Yohanna 9, wanda shi ma ya yi maganar warkar da wani makaho da Yesu ya yi ta hanyar amfani da miyau. Sai dai, a wannan lokacin, bai tofar da miyau a idanun mutumin ba; maimakon haka, ya haɗa miyau da ƙasa don ya zama laka, sa’an nan ya shafa wa mutumin lakar a idanu domin ya warkar da shi.

Mene ne yake faruwa a waɗannan al’amura? Shin Yesu yana amfani da magungunan gida ne don warkar da makanta waɗanda mahaifiyarsa ta koya masa tun a Nazaret? A’a, babu wani ikon warkarwa na musamman a cikin miyau ko lakar. Ba ni da masaniya game da dalilin da ya sa Yesu ya yi amfani da waɗannan hanyoyi, amma idan aka yi la’akari da warkaswa marasa adadi da Yesu ya yi ba tare da irin waɗannan hanyoyi ba, na san cewa ba ya buƙatar

yin amfani da miyau ko laka don ya sa waɗannan mutane su gani. Ikon ba da gani ba ya cikin miyau ko cikin lakar. Ma'ana, ikon ba ya cikin hanyoyin da aka bi—duk da cewa Yesu ya yi amfani da hanyoyi a lokuta biyun. Tasirin yana cikin ikon Allah ne wanda yake bayan waɗannan hanyoyi.

Abin da ya faru abu ne mai ban mamaki. Yesu ya tofar da miyau a idanun makahon, ya ɗora masa hannuwansa, sa'an nan ya tambaye shi, "Kana ganin wani abu?" Sai ya ɗaga kai ya ce, "Ina ganin mutane, suna kama da itatuwa da suke tafiya." (Markus 8:24).

Wannan wani babban ci gaba ne—mutumin ba ya iya ganin wani abu da yake tafiya *kafin* wannan gamuwa da Kristi. Wannan mutumi ya kasance makaho dundum. Yanzu aƙalla yana ganin wasu siffofi marasa fice, kamar inuwa suna motsi. Shin bai kamata mutumin ya gamsu da wannan ba?

Ban taɓa ganin mutanen da suke kama da bishiyoyi ba, amma na ga bishiyoyin da suke kama da mutane. Akwai wata babbar bishiyar oki a bayan kantin sayar da abinci na Wiegel sa'ad da nake girma, kuma kowace dare bayan duhu ya yi, a ƙarƙashin hasken wata, dole ne in bi ta hanyar daji da take bayan kantin don in isa gida na da yake kan titin McClellan Drive. Kowane dare nakan duba sama in ga inuwar wannan ƙatociyar bishiya, wadda take kama da tana da hannaye guda ɗari masu ban tsoro da suke miƙo don su kama ni. Nakan ruga da gudu in wuce wannan bishiya

domin tana kama da mutum—musamman mutum mai ban tsoro da ban kyamata. Amma ban taɓa ganin mutumin da yake kama da bishiya ba.

Taɓawa Ta Biyu

Me ya faru bayan haka? “Yesu ya sāke ɗibiya hannuwansa a idanun mutumin, sai idanunsa suka buɗe, ya sami gani, ya kuma ga kome sarai.” (st. 25). Da wannan taɓawa ta biyu daga Yesu, ganin mutumin ya buɗe sarai.

Manufar wannan labari ba wai don ya koya mana game da sake haihuwa ba ne. Manufar ita ce kawai a rubuta mana wani abin da ya faru a tarihi wanda ya nuna ikon Kristi wajen warkar da mutumin da yake fama da makanta. Amma ina tsammanin akwai wasu ƙa’idodi da za mu iya fahimta a nan. Ina tsammanin akwai kamanceceniya mai ma’ana da rayuwar Kirista wadda za a iya samu daga wannan bayani.

Da fari dai, sake haihuwa ba abu ne mai faruwa a hankali ba. Ba ya bukatar taɓawa biyu daga Kristi don a canza zuciyar mutum daga dutse zuwa nama. Ba ya bukatar taɓawa biyu na yatsan Allah don a fito da rai daga mutuwa. Taɓawa ɗaya kawai ake bukata.

Amma shin kun lura cewa sa’ad da aka sake haihuwarmu, sa’ad da aka farkar da mu a ruhance, ba a warkar da mu nan take daga dukkan zunubi ba? Bugu da ƙari, sake haihuwa farko ne, amma har yanzu muna ɗauke da wannan jikin mutuwa wanda

yake fafutuka da adawa da ran da Ruhun Allah ya samar a cikinmu. A ruhance, sa'ad da aka sake haife mu, mafi kyawun abin da za mu iya sa ran samu da farko shi ne mu ga mutane kamar bishiyoyi suna tafiya.

A can baya sa'ad da yayi da ake amfani da sitika mai taken "Na Same Shi" a jikin gaban mota ya yi ƙarfi, nakan ji ɗan haushi duk lokacin da na ga ɗaya. Na fahimci abin da taken yake nufi—mutane suna faɗar cewa sun sami lu'ulu'u mai daraja, abu mafi tamani a cikin wannan duniya. Duk da haka, sa'ad da Sabon Alkawari yake magana game da neman Allah da mulkin Allah, yana nufin Kiristoci ne. Burin neman Allah, da binciken samun Sa, yana farawa ne sa'ad da aka sake haihuwa. Sa'ad da mai neman ma'adanai ya sami guntun zinariya, shin daina nema yake yi? A'a, yana fara nema ne da ƙwazo fiye da kowane lokaci, kuma yana bincike a daidai wurin da ya sami na farkon, domin yana tunanin inda aka sami guntu ɗaya, dole ne a sami ƙarin wasu. Haka kuma, sa'ad da muka dandana sabuwar rayuwa, muna son ƙarin sabuwar rayuwa. Muna son mu yi girma. Muna son mu kai ga cikakken manyanta.

Lallai makahon ya yi farin ciki ƙwarai da ya ga mutane kamar bishiyoyi suna tafiya. Amma ina iya hango shi, da leɓunansa suna rawar jiki, yana cewa, "Yesu, muddin kana nan, ko za ka sake taɓa ni, domin ina so in ga komai sarai?" Sai Yesu ya sake taɓa shi, kuma kowane abu ya bayyana a sarari. Yanzu yana iya ganin mutane a matsayin mutane suna tafiya, bishiyoyi kuma a matsayin

bishiyoyi suna lilo a cikin iska. Yanzu yana iya rarrabe tsakanin mutum da bishiya, domin ya gani sarai.

Girma Cikin Alheri Yana Faruwa Ne Ta Wirin Hanyoyi Alheri

Sabon Alkawari yakan yi amfani da makanta a matsayin misali na mataccen yanayi na ruhaniya. Ta wannan kwatancin, sake haihuwa yana kama da ba mutum ikon gani ne. An lullube mu cikin duhu, amma haske ya keto cikin rayuwarmu kuma ba zato ba tsammani sai mu ga dadin al'amuran Allah, mu kuma ji dadin wadannan abubuwa da suke boye ga sauran mutane wadanda ba sa gane kyawunsu. Shin kuna da abokai wadanda ba za su iya fahimtar dalilin da ya sa kuke cike da matukar farin ciki game da bangaskiyarku? Kawai dai ba su iya ganinta. Ba za su iya fahimtarsa ba. Ba su fahimci abin da kuke magana a kai ba.

Amma mu ma ba mu ganinsa dalla-dalla ba. Muna bukatar a kara mana kaifin gani. Lokacin da aka sake haifuwarmu, ba tare da wata hanya ta matsakaici ba, ta wurin ikon Allah mai cikakken iko, wannan farkon ne kawai. Daga nan sai mu fara rayuwa ta girma a ruhaniya.

Domin mu gani sosai dalla-dalla, me ya kamata mu yi? Ba zan iya kiran Yesu ya zo ya sake taba idona ba—ko kuma, mafi dacewa, ya taba zuciyata ko raina. Haka ne, Yana nan ta wurin Ruhunsa, amma girman nan da za mu yi har mu kai ga manyanta yana faruwa ne ta hanyar wasu matakai da dole ne mu yi amfani da su. Wato, girma a ruhaniya ba ya faruwa nan take ba

tare da wani mataki ba, sai dai ana samunsa ne ta hanyar amfani da wasu matakai. Girma a ruhaniya yana bukatar yin amfani da abin da muke kira hanyoyin alheri—Littafi Mai Tsarki, addu'a, zumunci, da kuma shiga harkokin ikklisiya

Shin kuna son ku girma? Kuna son kaifin ganinku ya karu? To, dole ne ku kasance masu himma da horo wajen nazarin Nassin Littafi Mai Tsarki. Ta hanyar nazarin abubuwan da ke cikin wannan littafi, ganinku da fahimtarku za su kara fitowa fili. Idan kuna son ku kusanci Allah, dole ne ku yi magana da Shi, kuma hakan yana bukatar sadaukar da lokaci ga addu'a. Idan kuna son ku girma a cikin tsarkakewa, kuna bukatar ku kasance tare da Kiristoci wadanda suka fi ku manyanta kuma ku amfana daga zumuncin kasancewa tare da su. Idan kuna son ku kai ga manyanta a matsayinku na Kiristoci, dole ne ku shiga cikin harkokin ikklisiyar ku. Kasancewa memba na ikklisiya ba zabi ne ga Kirista ba. Kristi ne ya kafa ikklisiyar sa kuma ya umarci mutanensa su kasance sashenta, domin shiga harkokin ikklisiya (halarta, zama memba, hidima, bauta) wata hanya ce ta alheri. Wata hanya ce da ake raya sabuwar rayuwarku domin ku iya girma.

Muna Aiki Kuma Allah Yana Aiki

A takaice, idan kuna son ku wuce rudanin da har yanzu yake cikin ƙuruciyar rayuwar ku ta Kirista, dole ne ku yi aiki a kai. Mun gani cewa sake haifuwa aiki ne na Allah shi kaɗai (monergistic). Amma girma a rayuwar Kirista aikin haɗin gwiwa ne

(synergistic)—muna aiki zuwa gare shi tare da Allah. Me Sabon Alkawari ya ce? “ku ci gaba da yin ayyukan cetonku da tsoro da kuma rawan jiki,” (Filibiyawa 2:12b). Wannan kira ne zuwa ga aiki.

Akwai sassa da dama a cikin kunshin ceton. Yana farawa da sake haifuwa (wanda yake faruwa take yanzu), amma akwai wani aiki na bayyanarwa da dole ne ya faru, kuma wannan aikin na fitarwa za a yi shi ne ta hanyar yin amfani da dukkan ƙoƙarin da za mu iya bayarwa. Ba za mu iya kawai mu kwanta barci mu ce: “Allah cikin ikonSa ya kayar da ni daga kan dokina a kan hanyar Damascus. Shi ya fara; bar Shi Ya ƙarasa. Zan bar Shi Ya yi duka kawai..” A’a, an kira mu mu yi aiki domin cikar cetonmu da tsoro, ba tsoron firgita ba, amma tsoron kula da hankali da kwazo sosai.

Yayin da muke aiki, mun san wannan: “gama Allah ne yake aiki a cikinku, don ku nufa ku kuma aikata bisa ga nufinsa mai kyau.” (Filibiyawa 2:13). Za mu yi aiki ne kamar yadda Allah yake aiki. Ta wannan yanayi, abin da Allah ya fara a cikinku za a kawo shi ga kammalawa. Yesu Almasihu, wanda ya kama hannunku, ya fitar da ku, ya tofa yawu a idonku, kuma ya ba ku ganin da za ku ga abubuwan da a dā suke ɓoye gare ku, zai ci gaba da taɓa ku akai-akai domin fahimtar ku game da al’amuran Allah ta ƙara fitowa fili da kaifi. Amma dole ne ku yi aiki tare da Shi. Balagar Kiristancinka za ta kai wani matsayi gwargwadon yadda kake shirye ka yi aiki tukuru a cikin wann babban kira.

Sabon Haihuwa na Ruhaniya Dindindin Ne

Sa'ad da Allah ya tabbatar da sake haifuwarmu ta ruhaniya, ba Ya barin komai ya kashe wannan rai. Maimakon haka, waɗanda ya raya, yana kiyaye su kuma yana barin su da rai, domin wata rana su kai ga burin da ya sa ya sake haifuwarsu. Wannan shi ne ya sa Bulus ya gaya mana cewa "wanda ya fara kyakkyawan aikin nan a cikinku, zai kai shi ga kammalawa har yă zuwa ranar Kiristi Yesu." (Filibiyawa 1:6).

A cikin bincikenmu na koyarwar sake haifuwa, ko kuma haihuwa ta ruhaniya, mun gani zuwa yanzu cewa sake haifuwa ya zama dole, cewa abin asiri ne, cewa shi mafari ne kawai, cewa na ikon Allah ne, kuma cewa farat ɗaya ne yake faruwa. A cikin wannan babi, ina so in bincika wani fanni na sake haifuwa wanda sau da yawa mukan kasa yin la'akari da shi, wani fanni wanda yake sa mutane da dama ruɗani. Shi ne gaskiyar nan cewa sake haifuwa dindindin ne. Da a ce ya rage ga ikonmu ne, da za mu nemi kowace hanya da za mu iya don mu rasa sake

haifuwarmu. Amma Allah ba zai bar hakan ya faru ba; zai kai mu ga cikar fansarmu.

"Wa kuke cewa ni ne?"

Mutumin da ke cikin Sabon Alkawari wanda watakila ya fi kowa zama alamar dawwamar sake haifuwa shi ne manzo Bitrus. Amma ba a ko da yaushe ake kiran Bitrus da Bitrus ba; shi Siman ɗan Yona ne har sai da Yesu ya sake masa suna. Menene dalilin da ya sa aka ba shi wannan sabon suna?

A lokacin hidimar Yesu ta duniya, almajiran sun ɗauki lokaci mai tsawo tare da Shi. Sun sami damar kallon ayyukansa. Sun gan Shi yana warkar da marasa lafiya (Luka 8:40–48). Sun gan Shi yana kwantar da hadari (Luka 7:22–25). Sun gan Shi yana kwantar da hadari (Luka 7:22–25). Sun gan Shi yana tafiya a kan ruwa (Mat. 14:22–32). Sun gan Shi yana mayar da ruwa ya koma zuwa ruwan inabi (Yohanna 2:1–12). Sun gan Shi yana tada mutane daga matattu (Luka 7:11–17). Sun saurari koyarwarsa (Mat. 5–7). A taƙaice, sun sami damar ganin Yesu tare da wani mataki na kusanci wanda taron jama'a ba su more shi ba.

A wani lokaci na musamman a Kayisariya Filibi, Yesu ya janye daga taron jama'a ya kuma ɗauki lokaci tare da amintattun abokansa da almajiransa (Mat. 16:13–20). A wannan lokacin, Yesu ya ce musu: "Wa mutane suke ce da ni? Mene ne jita-jitar da ake yi a can waje? Shin sun gane kuwa har yanzu? Mene ne ra'ayin jama'a game da hidimaTa a yanzu?"

Ɗaya bayan ɗaya, almajiransa suka ba da amsoshi ga tambayar: “To, Yesu, wasu sun ce Kai Iliya ne, wasu sun ce Kai Yohanna Mai Baftisma ne, wasu kuma sun ce Kai annabi ne.” Yesu ya ce: “Wannan abin sha’awa ne. Amma ku kuna da fahimta ta kusa game da ko ni wane ne da kuma abin da nake yi. Menene ra’ayinku? Wa kuke cewa Ni ne? Me kuke tunani?” Siman ya yi Magana a madadin su goma sha biyu, ya kuma amsa tambayar da wannan furci: “Kai ne Kiristi, Ɗan Allah mai rai.” (aya 16).

Wannan wata sanarwa ce mai zurfi kuma mai ƙarfin zuciya daga bakin Bayahude. Bayahuden ƙarni na farko wanda yake kallon Yesu ya dube Shi ya ce, “Kai ne Almasihu.” Kalmar Turanci *Christ* ta samo asali ne daga Kalmar Girkanci *Christos,* wadda ke fassara Kalmar Ibrananci *Mashiyach*, ma’ana (“Almasihu”). Bitrus yana cewa ne a zahiri: “Kai ne Wanda mu Yahudawa muke mafarkinsa, muke addu’a a kansa, kuma muke begen zuwansa na tsawon ƙarnuka. Kai ne Wanda aka yi alkawarinsa ga Ibrahim, ga Dawuda, da kuma ga Irmiya. Kai ne Almasihu, Ɗan Allah mai rai.”

Bitrus Dutsen nan

Sa’ad da Yesu ya ji wannan furucin daga bakin Saminu, sai ya furta albarka. Ya kalli almajirinsa ya ce: “Mai albarka ne kai Siman ɗan Yunana, gama ba mutum ne ya bayyana maka wannan ba, sai dai Ubana da yake cikin sama.” (v.17). Ma’ana: “Saminu, ba ka kai ga wannan matsayar ta hanyar ikon basirarka kai kaɗai ba. Don ka ga abin da kake gani, ka fahimci abin

da kake fahimta, hakan na bukatar taimakon Allah. Allah ya bayyana maka wani asiri. Ya bayyana maka abin da sauran mutane suke rasawa kowace rana. Kana da albarka da kake ganin abin da kake gani."

Yana da muhimmanci sosai kada mu manta cewa Ruhu Mai Tsarki ne ya ba mu sabuwar haihuwa. Kada mu taba mantawa da wanda ya yi mana wannan abun da kuma irin albarkar da muke da ita na samun sabuwar haihuwa, wannan taɓawa daga hannun Allah. Kamar Bitrus, mun sami tabawar warkarwa ta Allah domin mu ga abin da wasu ba sa gani.

Sa'an nan Yesu ya juya ga almajirinsa ya ce, "Ina kuwa gaya maka, kai ne Bitrus, a kan wannan dutse zan gina ikkilisiyata" (st. 18a). An yi muhawara mai girma game da abin da Yesu yake nufi da wannan magana. Wasu suna gani cewa Yesu yana cewa zai gina ikilisiyarsa ne a kan Bitrus kansa, saboda haka wannan almajiri ya zama mai babban matsayi a Ikklisiya Katolika na Roma. Wasu kuma suna kallon wannan magana a matsayin nuni cewa Yesu zai gina ikilisiyarsa ne a kan wannan shaidar bangaskiya, domin duk wanda ya shaida cewa Yesu shi ne Almasihu ya kasance cikin ikilisiyarsa. Wato, dole ne mutum ya buɗe bakinsa ya ce, "Kai ne Almasihun." Kamar Yesu yana cewa ne: "Kai ne dutsen, Bitrus, wanda ya fara yin wannan shaida, kuma a nan ne za mu fara. Za mu fara gina ta yanzu, a nan take. Daga wannan gaba, zan gina ikilisiyata."

A Tace Shi Kamar Alkama

Hakika, kamar yadda muka gani daga baya a cikin bayanan Linjila, Bitrus bai rika yin hali kamar dutse a kowane lokaci ba. Abin mamaki ne ma da Yesu bai ce, “Kai burodin ne da ke gut-suttsurawa,” ko “Kai kamar kek ne mai laushi,” ko kuma “Kai kamar alewa mai taushi.” E, Bitrus ya sami lokutan da ya tsaya daram, amma a lokacin gwaji, ya yi matukar fãdiwa.

Bisa ga bayanin Luka game da daren cin amanar Yesu, sa’ad da Yake more bikin Ƙetarewa na ƙarshe, wanda kuma shi ne bikin Jibin Ubangiji na fari, sai Ya ce, “Ku ne waɗanda kuka dage tare da ni a cikin gwaji na, ni kuwa na ba ku mulki, yadda Ubana ya ba ni, domin ku ci ku sha a kan teburina a mulkina, kuma ku zauna a kan kujerun sarauta kuna yin shari’a ga kabilu goma sha biyu na Isra’ila” (Luka 22:28–30). Yesu ya gaya wa abokansa: “Kuna da aminci gare Ni, Ni ma zan kasance da aminci gare ku. Zan tabbatar da cewa kun zauna a kan kursiyan shari’a.”

Amma sai Yesu ya juya ga Bitrus ya ce: “Siman, Siman, Shaiɗan ya nemi izini ya sheƙe ka kamar alkama. Amma na yi maka addu’a, Siman, domin kada bangaskiyarka ta kāsa. Bayan ka juyo, ka ƙarfafa ’yan’uwanka.” (st. 31–32). Me ya kasance Yana faɗa a nan? “Siman, kana tsammanin kai dutse ne. Amma Shaiɗan yana son ka. Yana son ya tankaɗe ka. Yana son ya mayar da kai kamar laka a hannunsa. Yana son ya yi wasa da kai. Yana son ya yi amfani da kai a matsayin hanyar da zai same Ni. Na faɗa yanzu cewa kowa a nan ya kasance mai aminci gare ni,

amma kai, Siman, za ka ci amanata." Duk da haka, tare da wannan mummunan labari, Yesu ya ba wa Bitrus wannan tabbaci mai ban al'ajabi: "Amma na yi maka addu'a kada bangaskiyarka ta kāsa."

Yaya Bitrus ya amsa ga wannan gargaɗi mai ban tsoro? Ya ce, "Ubangiji, ina a shirye in tafi tare da kai har kurkuku, ko mutuwa ma." (k. 33). Sa'ad da na fara zama Kirista, wata ƙungiyar maza a kwalejinmu takan taru kowane daren Laraba don nazarin Littafi Mai Tsarki da kuma rera wakoki yayin da wani yake kada fiyano. Na koyi wakokin Kiristoci da yawa a karon farko a waɗancan daren, ɗaya daga cikin waɗancan wakokin kuwa ita ce "Inda Ya Kai Ni." Ina iya tunawa ina rera waɗancan kalmomi da dukkan kuzarin sabon tuba: "Inda ya kai ni zan bi; zan tafi tare da Shi, tare da Shi, duka hanyar." Sa'ad da na ji wannan waƙar yanzu, nakan ji laifi, domin ina son in yi hattara kafin in ce zan yi kowane abu ko in tafi kowane wuri. A cikin shauƙin kuruciyarmu, muna yin kowace irin fahari game da sadaukarwarmu da amincinmu wanda lokaci da juriya ne kawai za su iya tabbatarwa. Abin takaici, yayin da shekarun baƙuntarmu ke shuɗewa, muna koyon yadda muke da saurin kasawa.

Bitrus ya kasance kamar ni a cikin hanzarin kuruciyata. Ya kasance yana cewa: "Yesu, Kai ne Almasihu, Ɗan Allah mai rai. Inda Ka kai ni, zan bi. Zan tafi kurkuku tare da Kai idan ya zama dole. Har ma zan bi Ka har zuwa mutuwa." Bai riga ya koyi yadda yake da rauni ba.

Musu da Cin Amana

Bitrus ya yi furucin aminci mai ƙarfin gwiwa a cikin ɗakin sama a yammacin ranar Alhamis, daren da ya gabaci Ranar Juma'a Mai Tsarki. Ina Bitrus yake daga baya a wannan daren? Da zaran sojoji suka zo kama Yesu, Bitrus ya gudu. Ya fake a wajen gidan babban firist yayin da shugabannin Yahudawa suke ciki suna yi wa Yesu shari'a, yana ƙoƙarin samun wani labari game da abin da ke faruwa da kuma sanin makomar Ubangijinsa. Bayan haka wata yarinya mai hidima— ba shugaban masu tsaro ba, ba kuma shugaban rundunar tsaro ba —ta zo ta ce, "Kai ma kana tare da Yesu mutumin Galili." (Mat. 26:69), amma Bitrus ya yi musu. Daga baya, wata yarinya mai hidima ta ce, "Wannan mutum ma yana tare da Yesu Banazare." (aya 71), amma Bitrus ya yi musu tare da rantsuwa. A ƙarshe, wani mai tsaye a kusa ya ce, "Tabbatacce, kai ɗayansu ne, don harshen maganarka, ya tone ka." (aya 73). Shin Bitrus ya ce, "A'a"? Ba haka kawai ba. Littafi Mai Tsarki ya ce ya yi musu tare da la'ance-la'ance. Ya fara rantsuwa kamar ma'aikacin jirgin ruwa, yana nanata cewa shi bai san Yesu ba—duk domin tsoron waɗannan 'yan mata masu hidima da masu tsaye a kusa ya kama shi. Me ya faru? An tankade "Dutsen" kamar alkama. Lokacin gwaji ya zo, Bitrus kuma ya kāsa.

A farkon wannan daren, a Jibin Ubangiji, Yesu ya ce, "Gaskiya nake gaya muku, ɗayanku zai bashe ni." (Mat. 26:21). Almajiran da ke kewaye da teburin, suna kallon Yesu da fargaba, suka ce, ɗaya bayan ɗaya, "Ko ni ne, Ubangiji?" (aya 22).

Bayan haka suka zo kan mai ajiya na kudi. Yahuda ya ce, “Tabbatacce ba ni ba ne, ko, Rabbi?” Yesu ya amsa ya ce, “I, kai ma ka fada.” (aya 25). Yohanna ya ƙara da cewa Yesu ya ce, “Abin da za ka yi, sai ka yi shi da sauri,” nan take kuwa Yahuda ya fita zuwa cikin dare (Yoh. 13:27, 30).

Haka fa, Yesu ya sallami Yahuda zuwa ga amanar da zai ci. Nassin ya ce Yahuda ya riga ya amince zai ba da Yesu ga hannun maƙiyansa domin a biya shi azurfa guda talatin (Mat. 26:14–16; Mar. 14:10–11; Luk. 22:3–6). Da aka gama wannan aiki, Yahuda ya rataye kansa. Ya mutu cikin babban ƙasƙanci, ba tare da azurfarsa guda talatin ba, kuma da sunan da ya zama alamar cin amana ga dukan tarihin ɗan adam.

Mene ne bambanci tsakanin waɗannan mutane biyu? Amsar tana bayyana a cikin Addu’ar Yesu ta Babban Firist: “Yayinda nake tare da su, na kāre su na kuma kiyaye su ta wurin sunan nan da ka ba ni. Ba ko ɗayan da ya ɓace, sai dai wannan da aka ƙaddara zuwa ga hallaka don Nassi yă cika.” (Yoh. 17:12). A taƙaice, Yahuda bai taɓa samun sabuwar haihuwa ta ruhaniya ba, amma Bitrus da ne na Allah wanda aka sake haifarsa, saboda haka ikon Allah ya kiyaye shi. Sabuwar haifuwar Bitrus ta dindindin ce. Ko da yake Bitrus ya yi muguwar faɗuwa, mai ban tsoro kuma mai ban takaici, faɗuwarsa ba ta kasance ta gabaɗaya ko ta ƙarshe ba.

An kiyaye Bitrus ta wurin Wanda ya ba shi rai tun farko. Ruhu Mai Tsarkin nan shi ne tabbacin da Allah ya yi na cewa zai ba mu kome da ya yi alkawari (Afis. 1:14). Wasu lokuta

muna magana game da “kuɗin tabbaci,” wanda yake kama da biyan wani sashe na kudi tukunna. A cikin harkar cinikin fili ko gida, mai saye yana bayar da wasu kuɗin tabbaci, wanda ke nuna cewa shi mai saye ne da gaske wanda yake nufin ya ƙarasa cinikin. Haka nan kuma, sa’ad da Allah ya sake haifar wani ta wurin Ruhu, Yana ba da Ruhun ya kasance tare da wannan mutumin har abada. Kasancewar Ruhu “tabbaci” ce da ke nuna cewa a ƙarshe Allah zai ba wa wannan mutumin dukan abubuwan da ke tattare da sake haifuwa. Ko da yake Mutane wani lokaci suna kasa kamala cinikinsu duk da kudi tabbaci, Allah koyaushe yana yin abin da ya ce zai yi. Yana kammala yarjejeniyar. Yana gama cinikin. Ba ya taɓa kasa cika alkawari. Ba ya taɓa kasa biyan kudi. Sa’ad da Allah Ruhu Mai Tsarki ya ba ka rai, za ka iya tabbata cewa cetonka na dindindin ne.

Yi Murnar Sabuwar Haifuwa

Saboda haka muna murnar abin da ake nufi da sabon haihuwa. Babu wata kyauta mafi girma da ɗan adam zai iya samu. Babu wata taska mafi muhimmanci da ɗan adam zai iya mallaka. Idan ba za ka iya faɗa da tabbaci cewa an haife ka ta wurin Ruhu ba, ina rokonka ka tuna da koyarwar Yesu cewa sai dai idan an haifi mutum ta wurin Ruhu ba zai iya ganin mulkin Allah ba ko kuma ya shiga cikinsa (Yohanna 3:3, 5). Sai an sake haifar ka, in ba haka ba za ka rasa mulkin Allah. Amma idan an sake haifar ka, za ka san zakin alherin Allah da jinkansa. Za ka san ikon sabuwar rayuwa. Za ka zama sabuwar halitta, sabon halitta

wanda babu abin da zai iya halaka shi. Ba rayuwa, ba mutuwa, ba abubuwan da suke nan yanzu, ba abubuwan da suka shude, ba ikoki, ba manyan rundunoni, ba tsayi, ba zurfi, ko wani abu daban da zai iya raba ka da ƙaunar da ke cikin Almasihu (Rom. 8:38–39).

Dr. R. C. Sproul shi ne wanda ya kafa Ligonier Ministries, limami mai wa'azi da koyarwa na farko a Saint Andrew's Chapel da ke Sanford, Fla., shugaban farko na Reformation Bible College, kuma babban edita na mujallar *Tabletalk*. Har yanzu ana watsa shirye-shiryen rediyonsa na, *Renewing Your Mind*, a kullum a daruruwan gidajen rediyo a duniya kuma ana iya saurara a yanar gizo. Ya kasance marubucin littattafai fiye da ɗari, ciki har da *The Holiness of God, Chosen by God*, da kuma *Everyone's a Theologian.* An san shi a duniya baki ɗaya saboda kwararan hujjojinsa wajen kare rashin kuskuren Nassi da kuma buƙatar mutanen Allah su tsaya da tabbaci a kan Maganarsa.



Ma'aikatan Ligonier ƙungiyar tarbiyyar almajiran Kirista ce ta duniya wadda **Dr. R.C. Sproul** ya kafa a shekarar 1971 domin shelarwa, koyarwa, da kuma kare tsarkakar Allah a cikin dukkan cikarta ga mutane da yawa gwargwadon iko. Tambarin Laburarin Ligonier ya zama alamar amincewa a faɗin duniya da kuma cikin harsuna da dama.

Babban Umarnin Yesu ne ya karfafa Ligonier tana raba albarkatun tarbiyyar almajiranci a dukan duniya ta hanyar bugu da kuma tsarin dijital. Ana fassara ko sarrafa sauti na amintattun littattafai, makaloli, da jerin koyarwar bidiyo zuwa harsuna fiye da hamsin. Burinmu shi ne mu tallafa wa ikilisiyar Yesu Almasihu ta hanyar taimakawa Kiristoci su san abin da suka gaskata, dalilin da ya sa suka gaskata shi, yadda za su yi rayuwa bisa koyarwar, da kuma yadda za su raba shi.

Yaya mutum zai iya kasancewa an sake haifarsa?

Sa'ad da Yesu ya gaya wa shugaban Yahudawa Nikodimu cewa, “Dole ne a sake haifuwarka,” Nikodimu ya tambaya cikin mamaki, “Yaya waɗannan abubuwa za su iya kasancewa?” Kimanin shekaru dubu biyu bayan haka, har yanzu mutane suna rikice game da kalmar nan “sake haifuwa,” ko da yake mutane da yawa fiye da kowane lokaci suna da'awar cewa sun sami wannan gogewa.

A cikin wannan ɗan littafin, Dokta R. C. Sproul ya warware rikicewar kuma ya bayyana dalla-dalla ma'anar kasancewa wanda aka sake haifa. Dokta Sproul ya tabbatar da cewa sabuwar haifuwa tana da mahimmanci ga ceto kuma ya ci gaba da nuna cewa wannan sake haifuwa madaukakin aikin Allah ne a cikin zukatanmu.

Jerin ɗan littafin Muhimman Tambayoyi na Dokta R. C. Sproul yana ba da taƙaitattun amsoshi ga muhimman tambayoyi waɗanda Kiristoci da masu bincike masu zurfin tunani suke yawan yi.

Dokta R. C. Sproul shi ne wanda ya kafa Ligonier Ministries, ministan farko na wa'azi da koyarwa a Saint Andrew's Chapel da ke Sanford, Fla., kuma shugaban farko na Kwalejin Littafi Mai Tsarki ta Reformation. Ya kasance marubucin littattafai fiye da ɗari, har da littafin nan *The Holiness of God*.

LABURARIN LIGONIER

ADINI / Tauhidin Kiristan/ Koyarwar Ceto